# WASU DAGA CIKIN HALAYEN MAGABATA

(من أخلاق السلف)

Mawallafi

Sheikh Dr. Ahmad Farid

Fassarawa

Abubakar Muhammad Isa

Aminu Salisu

# Tarihin Mawallafi

Tarihin mai Fassara

Tsakure

Gabatarwar Marubuci

Gabatarwar mai fassara

# Abubuwan da littafin yaƙunsa

Tarihin Mawallafi ………………………………………………………………. i

Tarihin Mai fassara ……………………………………………………………… ii

Gabatarwar Mawallafi ……………………………………………………………. iii

Gabatarwar Mai fassara …………………………………………………………… iv

Godiya ……………………………………………………………………………. v

FASALI NA FARKO

Babi na ɗaya: Ikhlasi a wajen magabata …………………………………………… 1

Babi nabiyu:Takatsantsan na magabata wajen aiki da zance na Shari'ah ………… 2

Babi na uku: Mayar da al'amari zuwa ga Allah cikin al'amuran magabata …………

Babi na huɗu: Halayyar magabata ta barin munafurci ……………………………..

Babi na biyar: Halayyar magabata wajen haƙuri da juriya a kan zaluncin shugabanni ..

Babi na shida: Kishin magabata idan aka keta alfarmar Allah da kuma yadda suke bada kariya ga shari'a …………………………………………………

Babi na bakwai: Halayyar magabata wajen taƙaita murna akan abubuwan Duniya ……

Babi na takwas: Yadda magabata suke burin mutuwa idan fitina ta tunkaro su ………

Babi na tara: Yawaita jin tsoron Allah a cikin dukkan al'amuransu …………………

Babi na goma: Yadda magabata suke jin tsoron azabar Allah. ………………………..

FASALI NA BIYU

Babi na ɗaya: Raunin zuciyar magabata a halin rashin lafiya ………………………….

Babi na biyu: Yadda magabata suke damuwa da tuna mutuwa

Babi na uku: Ɗabi'un magabata wajen kawar da kai da kuma yafiya

Babi na huɗu: Ɗabi'un magabata wajen girmama addinin musulunci

Babi na biyar: Halayyar magabata wajen haƙuri

Babi na shida: Ɗabi'un magabata wajen gudun shugabanci

Babi na bakwai: Ɗabi'unsu wajen yiwa junansu nasiha

Babi na takwas: Yadda magabata suke girmama na ƙasa da su da kuma na sama da su.

Babi na tara: Ɗabi'un magabata wajen jin tsoron mummunar cikawa

Babi na goma: Halayyar magabata wajen lazimtar sallar dare a lokacin sanyi da zafi

## FASALI NA UKU

Babi na farko: Halayyar magabata wajen bincikar kansu da kuma kuɓutar da kansu daga siffar munafukai

Babi na biyu: Ɗabi'un magabata wajen gabatar da ayyukan lahira akan na duniya.

Babi na uku: Ɗabi'un magabata wajen yawan ambaton Allah da salatin Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi a duk inda suka zauna.

Babi na huɗu: Ɗabi'un magabata wajen yawan kuka domin sakacinsu a kan haƙƙin Allah

Babi na biyar: Yadda magabata suke jin taƙaituwarsu wajen biyayya ga Allah

Babi na shida: Halayyar magabata wajen nisantar gine-gine na ƙasaita

Babi na bakwai: Halayyar magabata wajen rashin ganin ƙimar duniya da gudunta

Babi na takwas: Halayyar magabata wajen rashin ɓarna a kan abin da yake halal ne

Babi na tara: Ɗabi'un magabata wajen rashin ganin yawan ayyukansu na gari

Babi na goma: Halayyar magabata wajen kwaɗayin ɗora mutane a kan hanyar alheri da tsoron bacin ayyukansu.

# FASALI NA HUDU

Babi na farko: Halayyar magabata dangane da tambayar halayen da 'yanuwansu suke ciki

Babi na biyu: Ɗabi'un magabata wajen yaƙar sheɗan

Babi na uku: Halayyar magabata wajen nuna gazawarsu a wajen godewa ni'imar Allah

Babi na hudu: Halayyar magabata wajen takatsantsan a kan tsoron Allah

Babi na biyar: Na daga ɗabi'un magabata ɓoye laifin 'yanuwansu

Babi na shida: Halayyar magabata wajen ƙaunar junansu da nutsuwarsu da kuma taƙaita zancensu

Babi na bakwai: Halayyar magabata wajen zantukan hikima

Babi na takwas: Halayyar magabata wajen yawan azumi

Babi na tara: Halayyar magabata wajen rufe duk wata ƙofa ta gulma a wajen zamansu

Babi na goma: Halayyar magabata wajen nisantar wasuwasi a wajen alwala da ibadunsu

## FASALI NA BIYAR

Babi na farko: Ɗabi'un magabata wajen ɓoye sirrin 'yanuwansu.

Babi na biyu: Halayyar magabata wajen shagaltuwa da laifukansu akan na wasu.

Babi na uku: Halayyar magabata wajen taimakon 'yanuwansu wajen aikin Allah.

Babi na huɗu: Halayyar magabata wajen sakin fuska da farantawa juna rai.

Babi na biyar: Halayyar magabata wajen karrama baƙo da yi masa hidima.

Babi na shida: Ɗabi'un magabata wajen ƙin amsa gayyatar cin abincin da yake na haramun ne.

Babi na bakwai: Ɗabi'un magabata wajen yawaita sadaƙa da rana da kuma dare, a bayyane da kuma ɓoye

Babi na takwas: Halayyar magabata wajen riƙo da abokin da za su girmama shi.

Babi na tara: Halayyar magabata wajen rashin rigima da kuma mayar da maƙiyi zuwa masoyi.

Babi na goma: Halayyar magabata wajen gujewa ma'abota saɓo.

## FASALI NA SHIDA

Babi na farko: Halayyar magabata wajen ƙara ƙanƙandakai a duk lokacin da suka sami wata ɗaukaka.

Babi na biyu: Halayyar magabata wajen rashin barin duk abin da yake na falala ne ko da ba wajibi ba ne.

Babi na uku: Halayyar magabata wajen yawaita neman gafara da dare da rana

Babi na huɗu: Halayyar magabata wajen umarni da kyakkyawan aiki da kuma hani da mummuna

Babi na biyar: Halayyar magabata wajen nisantar jiji da kai.

Babi na shida: Halayyar magabata wajen yadda suke shirya tsayiwa a gaban Allah.

Babi na bakwai: Halayyar magabata wajen nesantar shiga kasuwa kafin koyon ilimi kasuwanci.

FASALI NA DAYA

## BABI NA ƊAYA: IKHLASI A WAJEN MAGABATA

Na daga cikin ɗabi'unsu Allah ya ƙara musu yadda suna yawaita Ikhlasi wajen neman ilimi da kuma ayyukansu. Haka kuma, suna yawaita tsoron afkawa cikin 'Riya'[1] a cikin dukkan al'amuransu.

Allah maɗaukakin sarki ya ce: ''*Ku saurara, ga Allah ne kaɗai addini ke tsarkaka"*[2]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Lallai Allah baya karɓar aiki sai wanda aka yi domin Shi (Allah), kuma aka nufe shi da shi"*[3]

Ibrahimat Taimi Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *"Alamar mai Ikhlasi shi ne wanda yake ɓoye kyawawan ayyukansa kamar yadda yake ɓoye munanansa".*

Ash-Sha'abi Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa:

*"Yana daga cikin halin malamai idan suka samu ilmi suna aiki da shi, idan kuma suka shiga cikin aikin sai su duƙufa tare da ƙauracewa mutane, yayin da suka duƙufa sai a daina ganinsu, idan aka daina ganinsu kuma aka neme su sai su gudu, saboda tsoron fitina ga addininsu ko tsoron faɗawa cikin 'Riya'".*

Fudail ɗan Iyyad Allah ya ƙara masa yadda yana cewa:

*"Idan kuka ga malami ko wani mai yawan bautar Allah yana farin ciki da ambatonshi a wajen Shugabanni da Attajirai da kuma mutumen kirki ku sani mai 'Riya' ne shi. Saboda ma'anarIkhlasi shi ne bawa ya yi amfani da iliminsa da kuma ayyukansa domin neman abin da yake wurin Allah Maɗaukakin sarki kaɗai''.*

Farin cikin mutum ga samun yabon mutane na daga cikin alamomin 'Riya'. Kuma shi yasa magabata na ƙwarai suke ƙidaya 'Riya' daga cikin manya-manyan laifuffuka.

---

[1]Yin aiki domin wanin Allah
[2]Suratu Zumar : 3
[3]Nasa'i 6/26

Domin 'Riya' tana cikin shirka ƙarama. Ya zama dole ka binciki kanka ɗan'uwa kan iliminka da ayyukanka, kuma ka yi kuka a kansu har idan ka fahimci Riya ta shiga cikin su. Domin duk wanda ya yi aiki don a gani, Allah zai sa a gani kawai, kuma wanda ya yi domin aji, Allah zai sa aji kawai, (sa'anan ba shi da sakamako na lada a Lahira). Muna rokon Allah ya yafe mana kurakuranmu duniya da lahira.

WANNAN BABIN YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA:

1. Allah kaɗai ake nufi a wajen neman ilimi da aiki.
2. Riya ko yin aiki ba don Allah ba na daga cikin mafi haɗarin aiki rayuwar musulmi.
3. Neman yabo ko girmamawa a kan ayyukan ibadah na daga ala-momin riya.
4. Ɓoye kyawawan ayyuka na daga alamar tsoron Allah da gudun riya.
5. Mumini na dogara ne kawai ga abin dake wurin Allah na sakamako, domin haka baya tozartar da kansa ga wani halitta.

## BABI NA BIYU

## TAKATSANTSAN ƊIN MAGABATA WAJEN AIKI DA ZANCE NA SHARI'AH

Na daga cikin halayar su yin taka tsan-tsan wajen sanin matsayin ko wanne aiki ko zance a cikin Kur'ani da koyarwar Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, domin gudun faɗawa cikin bidi'o'i.[4]Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Duk abin da Manzo ya zo muku da shi, ku riƙe shi, kuma duk abin da ya hane ku da shi ku barshi.'*[5]

Kuma Allah maɗaukaki ya ce: *"Waɗanda suke saɓawa umarninsa (Manzon Allah) su tsoraci wata fitina ko azaba mai radaɗi da ke iya samun su.'*[6]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce; *"Kashedinku da fararrun al'amura domin dukkan fararrun al'amaru (a addini) bata ne.'*[7]

Kuma Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Duk wanda ya aikata wani aiki ba tare da umarninmu a kan shi ba, to an mayar masa (ma'ana ba za a karɓa ba).*[8]

Haƙiƙa magabata sun kasance suna kwaɗaitar da mutane tsayuwa a kan Kur'ani da koyarwar Ma'aiki Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da kuma nisantar fararrun al'amura a addini (Bidi'o'i), tare da tsanantawa a kan hakan. Har ta kasance Amirul Mu'uminina, Umar bn Khattab (Allah ya ƙara masa yarda) yakan yi yunƙuri ko niyyar yin wani al'amari, sai waɗansu su ce masa: "Annabi bai aikata ba kuma bai yi umarni a kan haka ba'' take sai ya fasa.

---

[4] Fararrun al'amura wanda addini bai yarda da su ba, wanda Kur'ani ko Sunnah ba su zo da su ba.
[5]Al-Hashr: 7
[6]An-Nur: 63
[7]Ahmad (4/126,127), Abu Dawud (12/359,360), da Thirmidhi (10/144) kuma ya inganta shi. Ibn Majah (43), Darimi (1/44 da 45 a babin "ittiba'us-sunnah), Bagawi (Sharhus-sunnah 1/205 sannan ya ce hadisi ne Hasan. Albani ya ingantashi a cikin Azzila)
[8]Muslim (12/16) cikin babin Ak'diya, Bukhari (5/301) a sulhu.

Wani daga cikin magabata yana cewa "Lallai hanyar mutane managarta ita ce iyakantuwa da koyarwar Kur'ani da kuma koyarwar Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi Kamar yadda zinare da jauhari ke da iyaka a tsakanin su.

Don haka, kowanne motsi ko shirunsu na ƙunshe ne da niyya managarciya a kan ma'aunin shari'ah. Babu mai fahimtar haka sai wanda ya zurfafa a cikin ilimin shari'ah.

WANNAN BABIN YANA KOYAR DA MU ABUBUWA KAMAR

1- Lallai ya zama dole dukkan ayyuka da zantuka su dace da karantarwar shari'a.

2- Barin kowan ne aiki ko zance idan sun saɓawa Shari'a.

3- Tsawatuwa da barin kowacce irin Bidi'ah a addini.

4- Kyawun musuluncin mutum tsayuwa a kan dokokin shari'a. Yin nasiha da wa'azi ga shugaba yayin kuskure ko ganganci.

## BABI NA UKU

## MAYAR DA AL'AMARI ZUWA GA ALLAH CIKIN AL'AMURAN MAGABATA

Na daga cikin halayen magabata yawaita mayar da al'amuransu da na iyalansu da kuma abokanansu ga Allah Maɗaukakin sarki. Babu wani abu da suke nema face suna masu dogoro ga Allah. Allah maɗaukakin sarki ya bada labari dangane da halin Muminin da ke gidan firauna in da ya ce:

*"Ina mai mayar da al'amari na zuwa ga Allah, lallai Allah masani ne game da bayinsa. Sai Allah ya tsare shi daga mummunan makiricin da suka shirya, kuma ya riskar da mummunar azaba ga Fir'auna da mabiyansa"*[9]

Kuma Allah maɗaukaki ya bada labari game da sahabban Annabi inda ya ce:

*" Su ne waɗannan da wasu mutane suka ce musu lallai ne wasu mutane (wato kafirai) sun taru a kanku, ku tsorace su, hakan sai ya ƙara musu imani suka ce, Allah ya isar mana; madallah da mai wakilci Allah, sai suka dawo da wata ni'ima da falala daga Allah ba tare da wata cuta ta shafe su ba"*[10]

A cikin bayanan da suka gabata, Allah ya bayyana sakamakon mayar da al'amura gare shi. Saboda haka, magabata ke cewa babu wani abu mafi amfani ga 'ya'yan malamai da nagartattun bayin Allah fiye da addu'o'insu zuwa garesu a lokacin da basa nan, tare da kuma mai da al'amuransu zuwa ga Allah.

Daga cikin abin da ke nuni zuwa ga falalar mayar da al'amura da kuma tawakkali zuwa ga Allah Maɗaukakin sarki, shi ne abin da Abu Hurairah Allah ya ƙara masa yadda ya rawaito daga manzon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi cewa:

---

[9]Ghafir: 44, 45

[10]Ali'Imran: 173, 174

"Wani mutum daga cikin ‘ya’yan Isra’ila ya tambayi waɗansu daga cikin ‘ya’yan Isra’ila da ya bashi rancen dinare dubu, sai ya ce, ka kawo min shaidu da zan kafa, sai ya ce, Allah ya isar min shaida, sai ya ce, ka zo min da wanda zai tsaya maka, sai ya ce, Allah ya isar min da zama mai tsayuwa gare ni, sai ya ce, ka zo min da mai lamuncewa, sai ya ce, Allah shi yafi isa da zama wakili, sai ya ce, ka yi gaskiya. Daga nan sai ya bashi kuɗin zuwa wani lokaci da suka sanya. Bayan haka sai ya tafi kogi domin biyan buƙatarsa, sai lokacin biyan bashin ya riske shi, don haka ya nemi abin hawa da zai mayar da shi domin cika alƙawarin wa’adin da suka yi amma sai bai samu ba. Ana cikin haka sai ya sami kututturen itace ya fafe shi ya zuba dinare dubun da ya ranta a ciki tare da wasiƙa zuwa ga wanda ya ba shi rancen, ya haɗa ya ɗaure wuri guda, sai ya zo bakin kogi ya ce ya Ubangiji ka sani cewa na nemi rancen dinari dubu wajen wani sai ya tambaye ni wanda zai tsaya min na ce masa Allah ya ishe ni, ya yarda da kai, ya kuma tambaye ni shaida na ce masa Allah ya isar mini zama shaida, ya kuma yarda da kai, ni kuma na yi ƙoƙarin samun abin hawa domin kai masa haƙƙinsa amma ban samu ba. Lallai ni yanzu zan ɗora maka nauyin isar da shi (saƙon) zuwa gare shi, sai ya jefa itacen cikin kogi, yana tsaye zuwa lokacin da ya yi nisa, sa’anan sai ya juya ya tafi yana neman abin hawa da zai koma garin su. Sai wanda ya ranta masa kuɗin shi kuma ya fita yana duban ko mahaya sun zo da dukiyarsa! A daidai lokacin sai ga kututturen itacen da ke ɗauke da dukiyarsa a gabansa, sai ya ɗauko shi a matsayin makamashi zuwa ga iyalansa, bayan da ya fasa itacen sai ga kuɗi dinari dubu da wasiƙa daga wanda ya rantawa kuɗin, yana cewa ina maka rantsuwa da Allah na yi ƙoƙarin samun abin hawa domin in kawo maka kuɗinka, amma ban samu ba face hanyar da na bi wajen aiko maka da shi. Bayan sun haɗu Mai kuɗin ya ce, shin ko ka yi sakon wani abu zuwa gare ni? Ya ce, ina mai baka labari da cewa ban sami abin hawa ba, ba hanyar da zan bi ba domin na zo maka da shi. Mai dukiyar ya ce

lallai Allah ya kawo maka abin da ka turo da shi cikin kututturen itace, sai ya tafi da dinarin dubu yana shiryayye"[11]

WANNAN BABI YANA KOYARDA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Mayar da al'amura ga Allah da Tawakkali su ne hanyar nasarar Musulmi.

2- Mafi kyawun addu'a ga mutum a yi shi lokacin da bayanan.

3- Faɗin 'Hasbunallahu wa ni'imal wakil' kariya ce daga dukkan sharri.

4- Kyakkyawar niyya tana cikawa mutum burinsa.

[11]Bukhari (3/362 Fathi) da Ahmad (2/348).

Na daga cikin halayensu yin aiki ta hanyar dai-daita al’amuransu na ɓoye da kuma na bayyane cikin ayyukan alheri domin gujewa munafurci da kuma abin da zai kunyatar da su ranar lahira.

Wani daga cikin magabata ya yiwa Umar ɗan Abdulaziz nasiha da cewa: *“kashedinka ya Umar ka zama waliyyin Allah a bayyane kuma maƙiyinSa a ɓoye. Domin duk wanda bai dai- daita al’amuransa na ɓoye da kuma na bayyane ba munafuki ne. kuma munafukai suna ƙasan shinfiɗar wuta”.*

Waɗansu daga cikin magabata suna cewa: *“Kashedinku da jin tsoron Allah irin na munafukai.Sai aka tambayesu ya ya tsoron Allah irin na munafukai yake? Suka ce, shi ne ka ga jiki na cike da tsoron Allah amma zuciyar ba haka ba”.*

Don haka ka binciki zuciyarka shin al’amuran ka na ɓoye suna dai-dai da na bayyane ko a’a?

Ka yawaita yin istigfari kuma ka sani duk wanda ya bayyanawa mutane fiye da abin da ke cikin zuciyar shi munafuki ne.

Daga cikin siffofin munafukai sun haɗa da:

1. Kasala daga barin Sallah da kuma ƙarancin ambaton Allah, kamar yadda Allah Maɗaukakin sarki ya faɗa: *“Idan sun tashi yin Sallah suna tashi cikin kasala ne suna nunawa mutane (ayyukan su) kuma basa ambaton Allah sai dan kaɗan”* [12]

2. Yana daga cikin siffarsu umarni da munanan ayyuka da hani daga kyawawan ayyuka, kamar yada Allah Maɗaukakin sarki ya ce:

[12]An-Nisai: 142

*"Munafukai maza da mata sashinsu na jiɓantar sashi ne, suna umarni da munanan ayyuka kuma suna hani daga kyawawan ayyuka, suna damƙe hannayensu (wajen yin alheri), sun manta da Allah, sai ya manta dasu. Lallai munafukai sune fasiƙai"*[13]

3. Yana daga cikin siffarsu jiɓantar kafirai, kamar yadda Allah Maɗaukakin sarki ya ce: *"Ka yi bushara ga munafukai da cewa suna da wata azaba mai raɗaɗi. Sune waɗanda suke rikar kafirai a matsayin masoyansu koma bayan muminai, shin suna neman ɗaukaka daga garesu ne, lallai dukkan ɗaukaka na ga Allah gabaki ɗaya"*[14]

4. Yana daga cikin siffofinsu ƙin yarda da hukuncin Allah Maɗaukakin sarki kamar yadda Allah ya ce: *"Idan aka ce dasu (munafukai) ku zo ga abinda Allah ya saukar da kuma Manzonsa za ka ga munafukai suna kawar da kai daga barinka kawarwa"*[15]

5. Yana daga cikin siffarsu yin ƙarya da yaudara da ha'inci da kuma kangara a lokacin yin husuma, kamar yadda Manzo Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Abubuwa guda huɗu duk wanda ya kasance a cikin su ya zama tsan-tsar munafiki. Wanda kuma ya ɗabi'antu da wani daga cikinsu ya kasance yana da wani yanki na munafurci a tattare da shi har sai ya bar ɗabi'ar:*

- ✓ Idan yayi zance sai ya yi Ƙarya;
- ✓ Idan yayi alƙawari sai ya saɓa;
- ✓ Idan aka yi yarjejeniya da shi sai ya yi yaudara;
- ✓ Idan aka yi rigima da shi sai ya kangare"[16]

---

[13] At-Tauba: 67
[14] An-Nisa'i: 138-9
[15] An-Nisa'i: 61
[16] Bukhari (1/81), Muslim (2/46), Nasa'i (8/116)

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Cikakkiyar siffar munafuki shi ne karya, yaudara, ha'inci, da kangara.

2- Ikhlasi da rashin munafunci shi ne dai-daituwar abin da yake cikin zuciya da ayyukan bayyane ko zantukan mutum.

3- Tsarkake zuciya da aiki tare da yawan istigfari na daga cikin hanyoyin kubuta daga munafunci.

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN HAKURI DA JURIYA A KAN ZALUNCIN SHUGABANNI

Na daga cikin halayensu yawaita haƙuri kan zalumcin shugabanni bisa yardarsu da cewa hakan (zaluncin shugabannin) bai kai ga sakamakon zunuban da suke yi ba.

Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Kamar haka nan muke jibinta sashen azzalumai akan wani sashen"*[17]

Kuma Allah maɗaukakin sarki yana cewa: *"Idan muka yi nufin halakar da wata alƙarya sai mu umarci majiya daɗin cikinsu da suyi fasiƙanci, daga nan sai su can-canci kalmar azaba a kansu, daga bisani kuma sai mu halakar da ita halakarwa"*[18]

Umar Ibn Abdulaziz ya kasance yana cewa: *"Hajjaju bin Yusuf wata jarrabawa ce daga Allah wadda tayi dai-dai da zunuban da mutanen lokacin suke aikatawa"*

Wani mutum ya rubuta wasiƙa zuwa ga Muhammad ɗan Yusuf yana masa koken zaluncin shugabanninsu. Sai ya amsa masa da cewa: "Wasiƙarka ta same mu, kuma nasan bai ɓoyu ga ilminka ba ya kai ɗanuwana cewa, bai kamaci wanda ke aikata laifi ba ya yi zaton rashin aukuwar azaba ba. Kuma ni bana ganin halin da kuke ciki face sakamako ne na zunubanku.

Allah Maɗaukakin sarki yana yin azaba ne ga azzalumi ta hanyar wani azzalumin, sa'annan ya mai da su zuwa ga wuta dukkaninsu. Haƙiƙa Allah maɗaukakin sarki ya hana taimakon azzalumai ko karkatuwa zuwa garesu. Don haka ya ce: *"ka da ku karkata zuwa ga waɗanda suka yi zalunci sai kuma wuta ta shafe ku…"*[19]

---

[17]Al- An'Am:129
[18]Al-Isra'i: 16

[19]Hud:113

An tambayi Aɗa'u ɗan Abi Rabahin Allah ya ƙara masa yadda dangane da mutumin da ke aikin rubutu a wajen azzaluman shugabanni kuma baya ƙin karɓar abin da suka ba shi na arziƙi!

Sai ya ce: "Ina ganin yafi kyau da ya bar wannan aikin, ya cigaba da cewa ba kaji zancen Annabi Musa bane, cewar shi: *"Ya Ubangiji ni game da ni'imar da ka yi mini ban zamo mai taimako ga masu ɓarna ba"*[20]

Abdullahi bin Mas'ud Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: *"Duk wanda ya taimakawa azzalumi ko ya masa dabarar danne haƙƙin musulmi, Haƙiƙa zai haɗu da fishin Allah"*

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWAKAMAR HAKA

1- Haramcin taimakon azzalumi ta kowacce fuska.

2- Zunubi dalili ne da ke haifar da shugabanni azzalumai.

3- Yin haƙuri da tuba daga barin laifuffuka dalili ne na kubuta daga shuwagabanni azzalumai.

4- Babu kyau yin aiki ƙarƙashin azzalumi.

5- Azaba ta na aukuwa ne cikin mutane sanadiyar zunubansu.

[20]Al ƙasas:18

BABINA SHIDA

## KISHIN MAGABATA IDAN AKA KETA ALFARMAR ALLAH DA KUMA YADDA SUKE BA DA KARIYA GA SHARI'A

Na daga cikin halayyarsu taimako wajen tsarkake Shari'a ya yin da aka keta matsayin Allah. Sun kasance suna aiwatar da ayyuka ba tare da sun abokanci wani ba sai dai idan sun fahimci yardar Allah a ciki. Kuma ba su zama suna soyayya ko ƙiyayya da wani ba domin wata buƙata ta duniya ba. Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Abubuwa uku duk wanda ya kasance daga cikinsu zai sami ɗanɗanon Imani''*

i. Allah da manzonsa su kasance sun fi soyuwa a gare shi daga waninsu.
ii. Yaso mutum don Allah.
iii. Ya ƙyamaci komawa ga kafirci kamar yadda yake ƙyamantar a jefa shi cikin wuta.[21]

Kuma Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Duk wanda ya yi soyyaya domin Allah, ya yi ƙiyayya domin Allah, ya yi kyauta ko ya damƙe domin Allah, lallai imaninsa ya cika'*[22]

Waɗansu daga cikin magabata sun kasance suna cewa: abokata da mutanen kirki na samar da nagarta a zuciya. Ahmad ibn harb ya ce:

*"Babu abin da ke mafi amfani ga zuciyar bawa kamar mu'amalarsa da nagartattun bayi, da kuma lura da irin ayyukansu. Kuma babu abinda ke mafi cutarwa ga zuciya kamar yin hulɗa da mutanen kawai da kuma kallon burgewa zuwa ga ayyukansu".*

WANNAN BABIN YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA;-

1- Cuɗanya da yin hulɗa da mutanen kirki yana gyara zuciya.

---

[21]Bukhari (1/60) da At-Tirmidhi (10/91)
[22]Abu-Dawud (4656), Tirmidhi (9/323)

2- Cikar imani na nuna soyayya da kiyayyar mutum domin Allah ne kawai, Kamar yadda yin kyauta ko hani domin Allah kawai.

3- Nuna ƙyama da rashin yarda tare da bada kariya ga addini yayin da ake keta alfarma ko matsayin Allah, ko na addini na daga cikin ɗabi'ar muminai.

4- Rashin sha'awa ko damuwa bisa ga ayyukan da fasiƙai na gyara zuciya da ba ta kyakyawar natsuwa.

## BABI NA BAKWAI

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN TAKAITA MURNA AKAN ABUBUWAN DUNIYA

Daga cikin halayyar magabata akwai ƙarancin yin dariya da kuma rashin alfahari da wani abu na samun duniya. Sun kasance suna yarda da duk abinda suka samu na tufafi, na abin hawa, na aure, da kuma kowanne irin matsayi.

Saɓanin abin da yan duniya suke kai yau, sun kasance haka ne saboda tsoron kada ya zama rububinsu ga ni'imar duniya gaggautowa ce ga abinda zasu samu na ni'imar lahira.

Umar Ibn Khattab Allah ya ƙara masa yadda ya ce: *"Ba don ina tsoron kada a rage mini daga ladana ba, da nayi tarayya daku wajen daɗaɗan kayan rayuwarku, domin na ji yadda Allah maɗaukakin sarki ke aibata wasu mutane a faɗarsa, "kun tafiyar da daɗinku a rayuwarku ta duniya kuma kun more"*[23]

Daga cikin abin da bayin Allah suka bambanta da shi daga waɗansunsu shi ne fuskantuwarsu ga lahira da kuma shiri domin ƙalubalanta. Don haka kai ɗan'uwa sai ka lura da abin dake cikin zuciyarka na shagaltuwa da rafkanuwa daga abin da zai kusantar da kai zuwa ga Allah maɗaukaki.

Saboda haka kana da buƙatar yawaita yin istigfari. Waɗansu daga magabata sun ce *''idan zaka sami ikon da kada wani ya sha gabanka a wajen Allah (ma'ana aikata alheri) kayi ƙoƙarin aikata hakan.''*

Kuma waɗansu daga magabatan sun ce *"Idan kaga mutum na rigegeniya a kan al'amuran duniya to kai sai ka nuna masa yin rigegeniya a cikin addini (wato lahira)*".

Waɗansu daga magabata sun siffanta Al-Hassan Albasri da cewa Wallahi idan ya fuskanto ka ce kamar wanda ya dawo daga binne masoyi ko majiɓincinsa, kuma yayin

---

[23]Ahkaf: 20

da ya juya ka ce kamar wuta ce a kansa, yayin da kuma ya zauna ka ce kamar bawan da aka kamo za a sare masa wuya ne, kuma yayin da ya wayi gari ka ce kamar wanda ya zo ne daga lahira, idan kuma ya yi yammaci ka ce kamar mara lafiya ne wanda cuta ta dabaibaye shi.

Imam Hassan Albasri ya ce: "labari ya riske ni da cewa wani salihi ya wajabtawa kansa da cewa Allah ba zai ganshi yana dariya ba, har sai yasan makomarsa daga cikin gidaje biyu na lahira (Aljanna ko Wuta)" Hassan ya cigaba da cewa haƙiƙa mutumin ya tsayu ga alƙawarinsa har zuwa mutuwarsa a haka, ba wanda yaga dariyarsa da haka ya haɗu da mahaliccinsa (Allah).

WANNAN BABIN YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA:

1- Gujewa duniya da ƙawace-ƙawacenta domin lahira.

2- Tattali da kuma fuskantar lahira da rashin yarda da dukkan shagala.

3- Rigegeniya ta Haƙiƙa domin addini ko lahira ne kawai.

4- Gujewa yawan raha da dariya domin tunawa da azabar lahira.

5- Cika alƙawarin da aka yiwa Allah da sauran halittu.

## BABI NA TAKWAS

## YADDA MAGABATA SUKE BURIN MUTUWA IDAN FITINA TA TUNKARO SU

Daga halayyar magabata akwai yin burin mutuwa idan suka jiyewa kawunansu tsoron aukawa cikin fishin Allah yayin da suka yi la'akari da abubuwan da suke bujuro musu na aikata zunubi.

Duk da cewa Mumini ba a yaddar masa ba tun asali a addini da yayi burin mutuwa sai dai idan ya ji tsoron aukuwar fitina a cikin addininsa. Domin Mumini ba abin da rayuwarsa take kara masa sai alkairi.

Waɗansu daga magabata sun ce duk lokacin da rayuwar Mumini ta tsawaita, yana zama kamar ganimace a gare shi. An karɓo daga Abu Hurairah Allah ƙara masa yarda ya ce, Mazon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Ka da ɗayanku ya yi burin mutuwa, ko dai ya zama mai kyautata ayyukansa don haka jinkirin ƙarin alheri ne a gare shi. Idan kuma mai munana aiki ne jinkirin sai ya zama tuba a gare shi"*[24]

Kuma daga Abu Hurairah Allah ya ƙara masa yarda ya ce Manzon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Ka da ɗayanku ya yi burin mutuwa kuma ka da ya roƙi zuwan mutuwar kafin ta zo masa, domin idan ɗayanku ya mutu ayyukansa sun tsaya, don haka rayuwar Mumini bata tsawaitu ba face sai ƙarin alheri"*[25]

A wata ruwayar da Bukhari ya ruwaito daga Anas ɗan Malik, Manzon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Ka da ɗayanku ya yi burin mutuwa saboda wata rashin lafiya, idan babu makawa sai ya yi burin, to sai ya ce, ya Ubangiji ka*

[24]Bukari(10/127) Al-Mardah da Nasa'I (4/3) Al-Jana'iz

[25](Muslim:17/8).

*rayani idan rayuwar ta fi alheri a gareni ko ka amshi raina idan mutuwar ce tafi alheri a gare ni"*

Amma ya yin da fitintinu suka yawaita kuma Mumini ya ji tsoro a kan addininsa, a wannan lokacin an so ya yi burin mutuwa kamar yadda ya zo a cikin Hadisin da manyan Mala'iku suke tattaunawa, a cikinsa Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Ya Allah idan ka yi nufin jarrabta waɗansu mutane da fitina to ka karɓi rayuwata ba tare da ka jarrabce ni ba"*[26]

Babban Malami Muniruddin Al-allamah Addimashki a tsokacin da ya yi ga Hadisin da ya gabata ta wajen ɓangaren addu'a ya ce "tana daga cikin addu'o'in da suka ƙunshi ma'ana masu faɗi, kuma wadda ta ke ɗauke da alherai masu girma ga duk wanda Allah ya yi masa baiwar zurfafin fahimta a addini.

Dalili kuwa don kasancewarsa hujjah ce yankakkiya, mai nuni ga ingattacen imani a kan abin da ya yi addua zuwa gareta. Domin kuwa ya nuna yardarsa da ya rasa rayuwarsa ta hanyar sadaukar da ita domin kuɓuta daga fitina da za ta iya shafar addininsa kuma a ƙarshe ta zamar masa azaba dauwamammiya.

Ba don cewa shi cikakken Mumini ba ne da bai jefa rayuwarsa ta hanyar rasa ta ba. Wannan ya nuna shi Mumini ne wanda ya yi imani da Allah, da ranar ƙarshe, da kuma azaba da ni'imar lahira. Haƙiƙa ya kai matuka ga tsoron Allah ta yadda ya zaɓi mutuwa a kan hargitsattsiyar rayuwa mai cike da fitina.

Domin kuwa bai dace tunkarar doguwar fitina ba. Don haka idan fitina ta shafi waɗansu mutane shi Mumini ya san tsayuwarshi ta fuskar fitina ba zai samar masa da wani amfani ba ko da ya yardarwa zuciyarsa ta hanyar ɗaukar kalubalen.

Domin fishin Allah ta tsananta a kan su. Dalilin haka ya sa ya zama cikin shiri gabanin aukuwar fitinar, ta hanyar kiran Ubangijinsa mai cikakkiyar iko a bisa da ya kuɓutar

[26]Ahmad (5/343) da Tirmidhi (12/115,116)

da shi daga fitinar, kar wutar fitinar ta shafe shi, domin haka ya ƙi zaɓar duniya a kan lahira (Ahkamul Tamanniyatul Maut na Sheikh Muhammad Ibn Abdulwahhab).

Abu Hurairah ya kasance ya kasance yana cewa: *"Wani zamani na nan zuwa ga mutane a lokacin mutuwa za tafi soyuwa ga malamai fiye da jajayen zinare, har mutum zai zo ga ƙabarin ɗan' uwansa yana cewa kaico ina ma ni ne a kwance cikin wannan ƙabarin"*

Abdullahi Ibn Mas'ud ya kasance yana cewa: "Daɗaɗan duniya sun ƙare saura wahal-halunta, don haka yanzu mutuwa ce gatan dukkan musulmi'.

WANNAN BABI YANA KOYARDA ABUBUWA KAMAR HAKA:

1- Halaccin burin mutuwa yayin da fitintinu suka yawaita kuma aka ji tsoron lalacewar imani.

2- Rayuwar Mumini na cike ne da alkhairi.

3- Dogaro ga Allah da neman taimakonsa domin kuɓuta daga fitina.

4- Fifita addini da lahira a kan rayuwar duniya ɗabi'ar muminai ne.

# BABI NA TARA

## YAWAITA JIN TSORON ALLAH A CIKIN DUKKAN AL'AMURANSU

Daga halayyar magabata yawaita tsoron Allah game da halin da rayuwarsu take a farko da kuma yadda zata kasance a ƙarshe, a farkon rayuwarsu halinsu na tattare da tsoron zunubi da kuma azaba, a halin ƙarshen rayuwansu kuwa suna tsoron girman Allah da kuma mumunan ƙarshe. Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Duk wanda ya tsoraci tsayuwarsa gaban mahaliccinsa (ya bar zunubi) yana da sakamakon aljannah kashi biyu"*[27]

Allah maɗaukakin sarki kuma ya ce: *"Ku ji tsorona har in kun kasance muminai"*[28]

Manzo Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Duk (matafiyi) da yake tsoron dare zai yi sammako, kuma duk wanda ya yi sammako zai kai masaukinsa, don haka ku saurara lallai ƙadarar Allah na da tsada, lallai ƙadarar Allah ita ce aljannah"*[29]

Abu Turab Annakhshabi ya kasance yana cewa, yayin da mutum ya himmatu da barin aikata zunubi sai taimakon Allah ya zo masa ta kowace ɓangare. Abubuwa uku suna daga cikin alamun ɓacin zuciya:

i. Mutum ya fara jin rashin tsoro ko firgita daga zunubai.

ii. Mutum ya ji baya iya aiwatar da aikin ɗa'a da biyayya.

iii. Mutum ya ji rashin tasirin wa'azi a gareshi.

Imam Alhassanul Basri ya kasance yana cewa: *"Daga cikin alamar mutumin da ya tsunduma a cikin zunubi shi ne rashin jin nishaɗi a zuciya game da azumin nafila da sallar dare"*

[27]Ar- Rahman :46
[28]Ali-Imran: 175
[29]Tirmizi (10/227) da Hakim (4/308)

Waɗansu daga cikin magabata sukan ce, ba bu komai a cikin yin ɗa'a face sai haske da kwarjinin fuska da samar da soyayya a zukata da ƙarfafa ga gaɓɓai, da amintar da rayuwa, da samun shaidun mutane, ta hakan ne yake wadatarwa wajen barin zunubi.

Kuma babu komai a cikin zunubi face sai ƙyama da ƙunci a fuska da samar da duhun zuciya da ambato cikin tsinuwa da rashin karɓar sheda daga gareshi da rashin aminci a rayuwa da waɗannan abubauwa zunubi ya kai mutuƙa ya zama abin tsoro.

Allah yakan sanyawa dukkan mai biyayya gare shi da kuma mai saba masa wasu alamomi na farin ciki ga mai ɗa'a da kuma baƙin ciki ga mai saɓa masa. Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Lallai waɗanda suka ce Ubangijinmu shi ne Allah sannan suka tsayu a kan haka, malaiku na sassaukowa garesu (lokacin mutuwarsu) suna cewa dasu kada kuji tsoro kuma kada kuyi baƙin ciki"*[30]

Waɗansu daga cikin magabata game da wannan ayar ta Al-ƙur'ani sukan ce Mala'iku na faɗin haka ne ga wanda ya yawaita tsoronsa da damuwarsa ga Allah Maɗaukakin sarki, saboda abubuwan da ya yi sakaci akansu na bautan Ubagijinsa, amma duk wanda bai da damuwa ga abubuwan alheri da ya yi sakaci a kansu, Malaiku ba za su ce masa komai ba daga abinda suka cewa Mumini (kamar yadda ya zo a surah ta sama, Fussilat: 30).

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA; -

1- Biyayya ga Allah na samar da farin jini da kwarjini da kima a idon jama'a.

2- Damuwa da abubuwan dake zowa imani a farkonsa ko a ƙarshen rayuwa na daga cikin ɗabi'ar Mumini.

3- Niyya da himmatuwa da barin saɓawa Allah yana buɗe ƙofofin alkhairi.

4- Damuwa da sakankancewa a kan ayyukan alheri na daga cikin ɗabi'ar Mumini.

---

[30](Fussilat:30)

## BABI NA GOMA

## YADDA MAGABATA SUKE JIN TSORON AZABAR ALLAH

Daga cikin halayyar Magabata yawaita nuna damuwa da Allah da kada ya yi musu azaba domin abubuwan da suka aikata na zaluncin kawunansu da kuma zaluncinsu ga waɗansu, ko da kuwa zaluncin da suka yi na daidai da girman allura da suke ɗinki da ita.

Tsoronsu na ƙaruwa musamman idan ɗayansu ya rena ayyukansa managarta a idonsa, a lokacin nan tsoronsa da baƙin-cikinsa sai su tsananta domin a ganinsa ayyukansa na alheri sun ƙaranta, ba za su iya biyan haƙƙin masu husuma a kan shi ba a ranar ƙiyamah.

Domin tana yiwuwa ɗaya daga cikin waɗanda aka zalunta na dukiya ko na mutumci, ba zai gamsu da za a ba shi dukkan ayyuka managarta, na wanda ya zalunce shi. Manzon Allah ya ce: *"Duk wanda yake riƙe da wani abu da ya zalunta daga ɗan'uwansa na dukiya ko mutumci, lallai ya nemi su warware tun yanzu, kafin ranar da babu dinare ko dirhami, sai kyawawan ayyuka ko munana"*[31]

Abu Hurairah Allah ya ƙara masa yadda ya karɓo daga Manzon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

*"Kun san wane ne matsiyaci? Sai sahabbai suka ce, matsiyaci a cikinmu shi ne wanda ba shi da dirhami ko dukiya, sai Annabi ya ce musu, lallai matsiyaci a cikin al'ummata shi ne wanda zai zo ranar ƙiyama da Sallah da azumi da zakka, amma ya zagi wannan, ya ci dukiyar wannan, ya zubar da jinin wannan, sai a kwashi ladan kyawawan ayyukansa a bawa wannan, ai ta ɗiba ana bayarwa, a lokacin da ladan ayyukan*

[31] (Bukhari (5/101) Al-Mazaalim, da Tirmidhi (9/254) Siffatul Kiyama)

*alherinsa suka ƙare, kuma bai gama biya ba, sai a ɗebo zunuban sauran masu bin shi bashi sai a zuba a kansa daga ƙarshe sai a jefa shi cikin wuta"*[32]

An ruwaito daga Hassanul Basri ya ce: "Haƙiƙa an ruwaito cewa ya sauka ga Manzon Allah faɗar Allah: *"Duk wanda ya aikata mumuna za a saka masa da ita kuma ba zaka samu gare shi ba koma bayan Allah wani majibinci ko mataimaki"*[33]

Abubakar (R.A) ya ce: "Haƙiƙa masifah mai halakarwa ta sauka, har idan ya kasance wannan zance daga Abubakar Allah ya ƙara masa yadda wanda aka shaidar masa da samun aljannah to yaya ya wajaba zancen waninsa kenan zata kasance. Lallai ya ku taron muminai kuna da abin lura a kai kuma ku kasance masu tsawatuwa ko kun aminta daga azabar yini mai girma.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBAWA KAMAR HAKA:

1- Jin tsoro da damuwa da al'amuran da suka shafi haƙƙin mutane.

2- Azzalumai basu da mataimaki ranar ƙiyamah

3- Tsiya ko rashin arziƙi a lahira na da dangantaka da zaluncin da mutum ya yi ga waɗansu a duniya.

4- Duk wanda ya zalunci wani sai ya biya shi a lahira da ayyukansa na alheri ko ɗaukan zunuban wanda ya zalunta.

[32]( Muslim (16/136) Al-Birru Wassilatu, Tirmidhi (9/253,254) Abuwabuz-Zuhdi)

[33](An-Nisa'i:123)

# FASLI NA BIYU

## BABI NA ƊAYA

### RAUNIN ZUCIYAR MAGABATA A HALIN RASHIN LAFIYA

Daga cikin halayyar magabata in suna rashin lafiya sai su rinƙa jin kamar ransu ne zai fita, domin a zatonsu rashin lafiyar ita ce fitan su daga duniya. Kuma hakan ba zai ba su damar tuba ba ko biyan haƙƙoƙin mutane ba, da haka sai su tafi lahira suna masu laifi. Kamar bawan da ya gujewa ubangidansa bayan yawan saɓawar sa gareshi kuma daga bisani aka kama shi aka miƙa shi ga ubangidansa.

Hassannul Basari Allah ya ƙara masa yadda ya shiga wajen wani mutum yana shure-shuren fitar rai, sai ya ce: *"Tabbas wannan shi ne ƙarshen al'amari wanda ya kamaci a guje shi tun farko"*

Waɗansu magabata sun shiga wajen Ɗan Utubah a lokacin rashin lafiyar da ya rasu, a ciki sai suka ce masa, ya ya kake ji? Sai ya amsa musu ta hanyar waƙe, yana cewa:

"*Ni na fita daga duniya kuma ƙiyamata ta tsayu,*
*A gobe masu ɗaukan gawata za su raina ni.*
*Dangina kuma za su gaggauta tona ramin Kabari na,*
*Su shirya fitar da ni kuma masoyana su gaggautar ni zuwa ga masaukina.*
*Kai ka ce kamar basu taɓa sanin kamarni na ba,*
*Gobe yini na da dare na za su kawo ƙarshe akai na"*

Lokacin da mutuwa ta zo ma Ibrahim Al-nakha'i sai ya fashe da kuka. Sai aka ce masa me ya sa kake kuka? Sai ya ce: *"Ina sauraron ɗan saƙon da zai zo mini daga ubangiji, shin zai yi mini albishir ne da aljanna ko kuwa da wuta"*

Ɗan'uwana ka yi tunani da kanka, ka sani kai wanda za a bijero ne ga dawwama (rayuwan lahira) ba ka mallaki rayuwa guda ga kanka, don haka sai ka yawaita neman

gafara cikin dare da yini. Lallai Allah shi ke taimakon mu da shiriyar shi, kuma ya yi mana baiwa da dalilan samun rahamarsa.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Shagaltuwa da lahira musamman lokacin kowace irin rashin lafiya.

2- Komai nisan rayuwa zata koma ma Mahaliccin ta domin hisabi da sakamako.

3- Tunanin sakamakon lahira bayan mutuwa.

## BABI NA BIYU

## YADDA MAGABATA SUKE DAMUWA DA TUNA MUTUWA

Daga cikin halayyar magabata akwai yawaita lura da kuma yin kuka da damuwa ga al'amarin mutuwa musamman idan suka ga an wuce da gawa, ko yayin da suka tuna da mutuwa da magaginta da kuma mumunar cikawa sai zukatansu su girgiza.

Abu Hurairah Allah ya ƙara masa yadda ya kasance idan yaga an ɗauko gawa sai ya ce, tafi zuwa ga ubangijinki, muma muna nan tahowa a bayanki.

Makahul Addamashƙi ya kasance yana cewa idan yaga jana'iza: ku tafi da ita muma muna nan tafe. Ga wa'azi taƙaitacce kuma gamsashshe, kuma rafkanuwa mai muni, wanda ya tafi da farko bai san abin lura ga na ƙarshe ba.

Al'a'amash ya kasance yana cewa muna halattar sallar jana'iza ba ma iya tantancewa yakamata a yi ma ta'aziya, saboda kowa na cike da damuwa.

Sabitu ya kasance yana cewa muna halartar jana'iza baka ganin kowa face yana lulluɓe cikin kuka.

Hakan na faruwa ne saboda sun kasance suna tuna tasu mutuwar ne, don haka ba suna kuka ba ne akan wanda ya mutu, a'a sai dai suna kuka ne akan tasu mutuwar.

Abin da yafi dacewa ga wanda mutuwa mai ɗaukarsa ce, ƙabari makwancinsa, tsutsotsi abubuwan ɗebe kewansa, Mala'iku Munkaru da Nakiru abokan zamansa, kuma ƙabari matabbaciyan sa, cikin tumbin ƙasa mazauninsa, ƙiyama alƙawarinsa, Aljannah ko Wuta wajen shigarsa, da kada a same shi da wani tunani da ya wuce waɗannan, ko wani tattali face sai don waɗannan. Don haka ka sani kuma ka lura.

Kamar yadda magabata suka lura da mutuwa, ka yawaita kuka da alheni. Domin abin da ke a gabanka na tashin hankalin ba a iya kamarta shi. Muna rokon Allah rangwame a duniya da lahira.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA:-

1. Mutuwa babbar wa’azi ce ga masu hankali.
2. Dukkan Musulmi suna taruwa cikin damuwa guda.
3. Yawaita tuna mutuwa da makomar mutum na daidaita al’amura.
4. Tuna rayuwa cikin ƙabari, shi ya kamaci mutum ya damu da shi.

## ƊABI'UN MAGABATA WAJEN KAWAR DA KAI DA KUMA YAFIYA

Daga cikin halayar akwai su da yawaita yafiya da kuma kawar da kai ga dukkan wanda ya cutar da su ta hanyar bugu, ko ƙwacen dukiyarsu, ko cin mutumcin su da makamartan su.

Sun zama haka ne saboda aiki da umarnin Allah Maɗaukakin sarki inda ya ce:

*"Ka yi musu rangwame sa'anan ka yafe musu, lallai Allah na son masu kyautatawa"*[34]

Kuma Allah Maɗaukakin sarki a wajen yabawa bayinsa na gari ya ce: *"…… masu kamewa daga fishinsu kuma masu yafiya ga mutane lallai Allah na son masu kyautatawa"*[35]

Kuma suna ɗabi'antuwa da ɗabi'un Manzo Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi don haka basa nuna fishinsu yayin da aka baƙanta musu, suna nuna fishin su ne kawai idan an keta hurumin (dokokin) Allah Maɗaukakin sarki. Don haka duk wanda ya ɗabi'antu da wannan ɗabi'a mai girma zai kasance mafi kusanci zuwa ga rahaman fiyayyen mai jinƙai, kuma zuwa ga rangwamensa da gafararsa. Kamar yadda ya zo a cikin ingantacce Hadisi. Wani attajiri ya kasance yana bawa mutane bashi amma yayin da ya ga wanda ke cikin tsanani sai ya cewa yaran sa ku yafe masa da fatan Allah muma Allah ya yafe mana, da wannan shima Allah sai ya yafe masa. Jafar bin Muhammad Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: yin nadama akan yin yafiya, yafi soyuwa a gareni da inyi nadama akan aiwatar da fishi na.

An tambayi Malam Katada wani mutum ne yafi daraja? Sai ya ce wanda yafi su yafiya.

An rawaito cewa wani daga cikin magabata bawan sa ya fusatar da shi, fusatarwa mai tsanani, don haka ya ɗauki aniyyar ladabtar da shi. Sai bawan ya karanta masa faɗin

[34]Ma'ida 13

[35]Ali-Imran 134

Allah game da mutanen kirki, inda Allah ke cewa: "masu kamewa daga fishin su", sai Ubangidan bawa ya ce: 'na haɗiye kuma na danne fishi na'. sai bawan ya koma karanta masa faɗin Allah: "masu yafewa mutane" . sai Ubangidan bawan ya ce: 'na yafe maka' sai bawan ya koma karanta faɗin Allah " Allah na son masu kyautatawa" sai Ubangidan bawan ya ce: 'tafi na 'yantar da kai domin Allah'

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA;

1- Allah yana son masu yawan rangwame da yafiya ga mutane.

2- Ana son fishin mutum ya tsananta ne idan aka keta dokokin addini fiye da idan aka taɓa mutuncinsa.

3- Yin rangwame ga mutane musamman waɗanda ke cikin tsanani.

4- Girmama dokokin addini da tsayuwa akan su na nuna alaman cikakken imani.

Na daga cikin halayyarsu yawaita girmamawan su ga alamomin musulmai da kuma son alheri gare su. Domin haka na cikin alamomin addini da Allah ya umurta da a girmama su. Allah Maɗaukakin sarki ya ce: *"Duk wanda ya girmama alamomin addinin Allah na daga alaman tsoron Allah ne dake cikin zuciyar sa"*[36]

Haƙiƙa Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana girmama alfarmar musulmai a mafi girman taron da mutane suka halarta.

Misalin lokacin taron hajjin shi na bankwana ya ce: *"Lallai jinanen ku da dukiyoyin ku haramun ne a tsakanin ku kamar yadda wannan rana (Arafah) ta haramta gareku a cikin wannan watan (Zhul Hijjah) kuma a wannan garin naku (Makkah)"*[37]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi kuma ya ce: *Dukkan musulmi game da ɗan'uwan sa musulmi haramun ne jinin sa da dukiyar sa da mutumcinsa.* [38]

Abubakar Siddik Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: *"Kada ɗayan ku ya wulaƙantar da wani daga cikin ku (musulmi), domin ƙaramin mutum cikin musulmi babbane a wajen Allah"*

Abdullahi ɗan Abbas ya kasance yana cewa: *"Mafificin kyaun aiki shi ne girmama abokanan zama. Ya kasance yakan dubi Ka'aba sai ya ce 'Lallai Allah ya haram ta ki, ya ɗaukaka ki kuma ya girmamaki, amma Mumini yafi ki alfarma a wajen Allah maɗaukakin sarki"*

Ikrima ya kasance yana cewa: *"Kashedin ku da kada ku cutar da wani daga cikin malamai, domin duk wanda ya cutar da malami haƙiƙa ya cutar da Manzon Allah tsira*

[36] Hajj 32
[37] Muslim (9/182,183,184) Al-Hajj, Abu Dawud (5/375-377) Al Manasik da Ibn Majah (2/1025)
[38] Muslim (16/121)

*da amincin Allah su tabbata a gare shi"*

Don haka sai ka lura ɗan'uwa sai ka lura da kanka shin kana girmama alfarmar musulmai musamman malamai da managartan mutane kamar yadda aka ambata, ko kuwa kana wulaƙantasu tare da cin mutumcin su hakan yasa ka zama daga cikin fasiƙai.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA;

1- Wajibi ne girmama alfarmar musulmai tare da kuma so musu alkhairi.

2- Zubar da jinin musulmi, wulaƙanta shi ko cin dukiyarsa ya haramta.

3- Girmama Malamai da gujewa cutar da su na daga cikin kyaun Imani.

4- Alfarmar Mumini tafi alfarmar Ka'aba a wurin Allah.

5- Alamar fasiƙanci ne wulaƙanta ko cin mutumcin musulmi.

## BABI NA BIYAR

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN HAKURI

Daga cikin halayyarsu akwai haƙurinsu ga cutarwar matansu da kuma shaidawarsu da cewa dukkan abin da ya bayyana na saɓawan matansu garesu yana da kamarni da irin mu'amalan su da Ubangijinsu. Domin haka duk lokacin da ya saɓawa Ubangijinsa matansa ma zata saɓama masa.

Wani daga cikin magabata ya kasance yana cewa: "Ni ina fahimtar saɓawata ga Allah daga irin sauyin ɗabi'ar dabbata da matata"

Magabata sun kasance suna bayar da cikakken haƙƙoƙin mata amma hakan baya hana saɓawar matan gare su.

Ali ɗan Abi Talib Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: "Yana daga cikin samun nasarar mutum samun sa ga abubuwa biyar: na ɗaya dacewar sa ga Matar aure managarciya, samun 'ya'ya masu biyyaya, yan'uwa masu tsoron Allah, maƙwabta managarta da kuma samun arziƙin sa agarin su."

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Mafi alkhairin ku shi ne mafi alkhairi ga iyalan sa. Ni na fi ku zama mafi alkhairi ga iyalaina"*[39]

Ibn Harb Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: idan mace ta haɗa halaye guda shida Haƙiƙa ta cika nagartatciya: kiyayewarta ga Salloli wajibabbu biyar, biyayyarta ga mijinta, neman yaddar Ubangijinta, tsare harshenta daga gulmace-gulmace da kuma annamimanci, gujewarta daga ƙyal-ƙyalin duniya, da kuma haƙurinta lokacin jarabawa". .

Yana daga cikin halayen magabata ga matan su kuma da yin haƙuri wajen ganin kyautatuwarsu ta ƙoƙari bin umarnin Allah Maɗaukakin sarki a cewar sa:

---

[39]Tirmidhi (13/262)

*"Ka umarci iyalan ka da yin Sallah ka kuma yi haƙuri a kan haka"*[40]

Da kuma himmatuwarsu akan lura da haƙƙoƙin matansu na da ga cikin bin umarnin wasiyyar Manzo Allah da ya ce: *''ku ji tsoran Allah game da haƙƙin mata domin kun mallake su ne kan Amanar Allah don haka farjin su ya halatta gareku da Kalmar Allah (Umarnin sa)".*

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA;

1- Yin haƙuri da halayyar mata.

2- Bin umarnin Allah da rashin saɓama masa domin mallakar arziƙi

3- Kiyaye haƙƙoƙin mata na daga cikin cika amanan Allah ne.

4- Daga samun nasarar mutum akwai samun iyali managarciya

5- Alamar nagartar mace ita ce kula da haƙƙin Allah da na miji a kanta.

[40]Daha 132

## BABI NA SHIDA

## ƊABI'UN MAGABATA WAJEN GUDUN SHUGABANCI

Daga cikin halayyar magabata akwai su da barin neman shugabanci sai dai in tazo musu ba makawa ta hanyar mutane su gabatar da su akan kawunansu. Duk da haka sai kaji wani na cewa ni ban cancanci shugabanci ba, amma sai mutane su ce ka cancanta har ma da ƙari. Ɗabi'ar su ta kasance haka domin ƙoƙarin bin umarnin Manzo Allah Maɗaukakin sarki wanda ya ce: *"Ya kai Abdurrahman kada ka nemi shugabanci domin idan aka baka, saboda ka nema sai a bar ka da shi (ba tare da taimakon Allah ba) amma idan an baka ba tare da ka nema ba Allah zai taimakeka akai"*[41]

Kuma Manzon Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi Allah ya ce: *"Lallai ku zaku ƙaunaci shugabanci, amma da sannu zata zama nadama ranar Kiyamah, madalla da mai shayarwa (shugabanci) tir da mai yayewa (sauka daga shugabanci)"*[42]

Haƙiƙa Sufiyan Ath-Thauri Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: *"Duk wanda ya nemi shugabanci kafin a neme shi da shi zai kuɓuce masa kuma mutuwarsa tafi alheri a gareshi"*

Ya kuma kasance yana cewa: *"Kada ɗayanku ya nemi shugabanci face sai ya yi ƙoƙari ga kansa (Tarbiyantar da ita) na tsawon shekaru saba'in".*

Muslim Ibn Kutabahya ya kasance yana cewa: *"Mun riski mutane waɗanda suke ɗaukar yin shugabanci cikin mafi girman bala'o'i. Sai ga shi yanzu mun ga ana nemansa"*

Magabata idan sun ba da shugabanci ga amininsu sai su yi addu'a agare su da cewa:

*"Ya Ubangiji kamartar da shi ambaton mu har ya zamo kamar bai san mu ba muma bamu san shi ba"*

---

[41]Bukari (13/13)
[42]Bukari (13/125)

WANNAN BABI YANA KOYARDA ABUBUWA KAMAR HAKA;-

1- Ba’a son neman mulki har sai babu makawa.

2- Samun taimakon Allah ga mai mulkin da bai nema.

3- Shugabanci na da ga cikin musibu mai haifar da na dama ranar lahira.

4- Taimakon mai mulki shi ne kaura cewan mutane na kusa domin ya samu daman yin adalci.

## BABI NA BAKWAI

## ƊABI'UNSU WAJEN YIWA JUNANSU NASIHA

Daga cikin halayyarsu yin nasiha ga junan su, manyansu sun kasance ba sa gundura ko damuwa da yi ma ƙananansu nasiha. Wannan saɓanin abin da wawaye suke a kai yau kenan. Domin su magabata suna ƙoƙarin yin aiki ne da umarnin manzon Allah wanda ya ce: *"Addini nasiha ne' sai Sahabai suka ce, ya Manzon Allah gawa ne? ya ce ga Allah da littatafan sa, da manzannin sa, da shugabannin musulmi da jama'ar su"*

Magabata sun kasance suna karɓar nasihohi kuma suna godewa wanda ya yi musu nasihar, ba sa ganin wanin su cewa ya tsayu gaba da haƙƙin wanda ya yi masa nasiha ko ya dauki tsawon rayuwa yana masa hidima. Domin al'amuran da suka shafi Lahira ba sa daidaituwa da ƙaddarorin duniya.

Wani mutum ya cewa Hassanul Basari ka yi mini nasiha. Sai ya ce masa ka girmama al'amarin Allah a duk inda ka kasance, shi ma Allah zai girmama ka a duk inda kake.

Waɗansu daga cikin magabata sun kasance suna rubutawa junansu nasiha ko da ko gidajen su sun nisanta da juna. Kuma waɗanda aka yiwa nasihar yakan karɓi nasihar kuma ya godewa wanda yayi masa nasihar.

Saɓannin halin da mutane suke ciki a yau, wanda abu ne mai wuya ka yi wa wani nasiha face shi kuma ya koma yana neman aibinka domin ya auka maka.

Ɗawus ya rubuta wasiƙa zuwa ga Makhul ya ce masa: Bayan sallama, ya ɗan'uwa ka kiyayi zato, kana da wani matsayi mai girma a wajen Allah, saboda abin da ya bayyana agareka na ayyukanka, domin duk wanda ya yi irin wannan zato ga kansa zai je lahira ba shi da komai na alheri.

Kodayake so da yawa mutane sukan girmamaka saboda ayyukanka da suke gani na gari, kai kuma ka gaggauta ladan ayyukanka da haka. Ka sani ɗan'uwana! Ka yi wa

kanka nasiha da farko sannan sai ka yiwa sauran yan'uwanka ta hanyar bayani kuma a rubuce. Ahir ɗinka ka da ka wahalar ko tozartar da wanda ya yi maka nasiha.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA;-

1- Ana karɓar nasiha daga kowa, ƙarami ko babba, mai arziƙi ko talaka, mai mulki ko wanda ake mulka, namiji ko mace.

2- Duk nasiha kada ya ƙetare dokokin Allah da Manzonsa.

3- Girmama wa da nuna ƙauna ga duk wanda ya yi nasiha.

4- Buƙatuwar kowa zuwa ga nasiha

5- Rashin damuwa da yarda da yabo akan ayyukan alherinka.

BABI NA TAKWAS

YADDA MAGABATA SUKE GIRMAMA NA KASA DA SU DA KUMA NA SAMA DA SU

Daga cikin halayyarsu akwai kyakkyawan ladubansu ga ƙananansu ballantana zuwa ga manyansu, kuma da kyawawan ladubansu ga na nesa ballantana ga na kusa, Kamar yadda kyawawan ladubansu ga jahilai ballantana ga masu ilmi. Allah maɗaukakin sarki ya umarci Annabi Musa da Haruna da su yi zance mai taushi ga Fir'auna, sai ya ce: *"Ku yi masa magana tattausa"*[43]

Duk da cewa Fir'auna shi ne mafi zama ɗan tawaye cikin kafirai. Sai su ka haɗu akan cewa maɗaukakiyar daraja tana kasancewa ne tare da ƙaruwar ladabi. Kuma a asali ladabi shi ne ji ga kai rashin cika da gazawa a rai kuma da ganin cika ga wani, saɓanin wanda yake kallon kansa da idon cika, waninsa kuma da idon tawaya, domin hakan yana gadar da girman kai, Allah ya tsare mu. Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"An aiko Ni ne domin in cika kyawawan ɗabi'u".*

Ali ɗan Abi Ɗalib ya kasance yana cewa: mafi sanin mutune ga Allah shi ne mafi tsanancin su wajen girmama masu cewa, "La ilaha illallah". Bakru Ibn Abdullah Al-Muzni ya kasance yana cewa, idan ka ga wanda ya girme ka, ka girmama shi, ka kuma ce, wannan ya riga ni shiga musulunci da kuma aika ta ayyukan nagarta.

Amma yayin da ka ga wanda ka grime shi sai ka ce a cikin zuciyarka wannan na riga shi wajen aikata zunubi. Idan mutane suna girmamaka ka ce, wannan na daga cikin falallar Allah a kai na wanda ban cancance shi ba, idan sun wulaƙanta ka ka ce, wannan saboda zunubin da na yi ne. kuma ka sani idan ka jefi Karen maƙwabcinka da tsakuwa ka cutar da maƙwabcinka.

---

[43](Daha 44)

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA;-

1. Ladabi da girmamawa ɗabi'ar mutanen kirki ce.
2. Wa'azi da shiryar da mutane na buƙatar girmamawa da kuma ladabi zuwa gare su.
3. Mafi girma da kyaun musuluncin mutum na tattare ne da kyawawan halaye.
4. Rashin girman kai da kuma ganin tsarkaka ko fifiko akan waɗansu na daga cikin siffar mutanen kirki.

# BABI NA TARA

## ƊABI'UN MAGABATA WAJEN JIN TSORON MUMMUNAR CIKAWA

Daga halayyarsu akwai tsananin tsoronsu ga Allah Maɗaukakin sarki da kada ya karɓi rayukansu a halin suna cikin munana ayyuka, wanda zai sa su zama cikin waɗanda za a tsare su daga ganin Allah kuma akai su wuta daga ƙarshe.

Domin haka sai mutum ya tsunduma cikin tunani da damuwa a kan haka har ya kasance ba a ganin sa. Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Lallai ana la'akari ne da ƙarshen ayyuka"*[44]

Kuma Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Lallai akan sami mutum ya yi ta aiki irin aikin 'Yan aljanna har sai ya zamo tsakanin sa da ita bai wuce kamu ɗaya ba, sai ƙaddararsa ta rinjaye shi, sai ya yi aiki iri na 'Yan wuta kuma ya shige ta"*[45]

Wannan irin halin shi ke mantar da kuma ɗimautar da hankalin mutum, a kan haka ne Sayyidah Aisha Allah ya ƙara mata yadda take cewa: Mutum zai iya yin aiki na lokaci mai tsawo irin na 'yan aljanna alhalin kuwa shi ɗan wuta ne. Sau da yawa waɗansu fuskokin da ke nuna tsoron Allah amma sun faɗa cikin ayyukan irin na labarin waɗanda ayyukan su wahala ne kawai kuma za su ƙonu a cikin wuta mai zafi.

Sau da yawa wanda abin hawansa ke kusa da gaban kogi gab da ya kuɓuta, amma yayin da ya himmatu da hawa domin kuɓuta sai igiyyar ruwa ta bugo shi sai ya nutse a ciki.

Don haka kowa ne bawa (mutum) na ƙarƙashin irin wannan haɗarin. An karɓo daga Anas Ibn Malik Allah ya ƙara masa yadda ya ce: Manzon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana yawaita faɗar:

---

[44]Bukhari (11/499)
[45] Bukhari da Muslim

*"Ya mai jujjuya zukata ka tabbatar da zuciya ta akan addinin ka" sai na ce ya Annabin Allah, mun yi imani da kai da abin da ka zo da shi, shin ka na jin tsoro ne akan mu? Sai ya ce; "eh, domin zukata na tsakanin 'Yan yatsu na daga Yatsun Allah yana jujjuyan su yadda yake so"*[46]

Muɗarrif ɗan Abdullah ya kasance yana cewa: "Ni ba na mamakin wanda ya hallaka kuma yaya ya hallaka, amma ni na kan yi mamakin wanda ya tsira ne da yadda ya tsira. Lallai babu ni'ima da Allah ya ni'imta ta ga mutum fiye da karɓar rayuwar sa a cikin musulunci.

WANNNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA:

1. Duk kyuan aikin mutum in bai nufi Allah ba zai yi mummunar ƙarshe.
2. Yawaita rokon Allah tabbata a cikin musulunci har mutuwa.
3. Mafi girman ni'ima da Allah zai wa bawa shi ne ta ƙarshe shi a cikin musulunci.

[46]Tirmidhi (8/307)

## BABI NA GOMA

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN LAZIMTAR SALLAR DARE A LOKACIN SANYI DA ZAFI

Daga halayyarsu akwai dagewarsu ga tsayuwar dare wajen bautar Allah lokacin zafi da sanyi. Saboda ƙoƙarinsu wajen bin umarnin Manzon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi wanda ya ce:

*"Ina horan ku da Sallah dare, domin shi ne halin managarta bayin Allah da suka zo kafin ku, kuma shi ne mai kusanci ga ubangijinku, kuma mai kankarewa ga munanan ayyukanku, kuma mai haninku ga aikata laifuffuka, sannan kuma mai korewa daga cututtukan da ke jikinku"*[47]

Abdullah ɗan Mas'ud ya kasance yana tashi domin sallar dare yayin da idanuwa suka rufe, sai ana jin wata irin ƙara kamar kukan kudan zuma har gari ya waye.

Ya kasance ana shinfiɗawa Abdul-Aziz ɗan Abi Dawud shinfiɗa, sai ya ɗora hannayensa a kai, kuma ya ce: ''Mamakin laushin wannan shinfiɗar!, sai dai shinfiɗar Aljanna ta fi ki laushi.'' Daga nan sai ya tashi domin Sallah ba zai gushe yana Sallah ba har sai alfijir ya bayyana.

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana yin Sallah har digadigansa su kumbura kuma ƙaurukansa su yi nauyi, sai ace masa "me yasa kake aikata haka bayan an yafe maka zunubanka da suka gabata da waɗanda suka jinkirta" sai ya ce ba zan zama bawa mai godiya ba. Bukhari ne ya ruwaito shi.[48]

Hasanul Basari ya kasance yana cewa: wani bai taɓa barin tsayuwar dare ba face sai don zunubin da ya aikata. Ya kasance sau da yawa yana cewa "tsayuwar dare kan yi wuya ne ga wanda laifuffukan shi suka yi nauyi.

---

[47]Tirmizi (13/64,65)

[48]Bukhari (3/14)

Kuma ya kasance, Mutum kan yi zunubi sai Allah ya haramta masa damar tsayuwar Sallar dare. Hakanan ya kan ce idan ka ji ka kasa yin tsawuwar dare da yini da azumi to ka sani kai wanda aka haramta maka ne saboda laifuffukanka da zunubanka su suka dabaibaye ka.

Abdullahi Bin Mubarak Allah ya yarda da shi ya ruwaito daga matar Masruƙ ta ce: "Masruƙ bai kasance yana jin damuwa ba ko da kwaurukansa sun kumbura saboda dogon tsayuwar Sallah. Nakan zauna a bayansa ina kuka domin tausayin sa.''

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Zunubai suna haramta mutum samun damar bautan Allah musamman yin tsayuwar dare.

2- Tsayuwar dare na samar da yardar Allah kuma ya kankare zunubai.

3- Yin tsayuwar dare hanya ce na nuna godiya ga ni'imar Allah.

4- Tsayuwar dare na buƙatuwa zuwa ga lizimta da haƙuri.

FASALI NA UKU

BABI NA DAYA

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN BINCIKAR KANSU DA KUMA KUƁUTAR DA KANSU DAGA SIFFAR MUNAFUKAI

Daga cikin halayyarsu akwai yawan bincikan zukatansu kowane lokaci domin fitar da dukkan siffan munafunci daga cikin ta kuma da ƙoƙarin shigar da kishiyoyinta na daga siffan mumunai. Yana daga cikin yawan siffofin muminai wanda Allah Maɗaukakin sarki ya ambata a cikin littafinsa mabuwayi. *"Su ne masu yawan tuba kuma masu yawan yin ibadah"*[49]

Haka kuma faɗinsa maɗaukakin sarki cewa: *''Lallai muminai sun rabauta, su ne waɗanda game da sallolin su suna da khushu'i (natsuwa da tsoron Allah[50])''.*

Akwai ayoyi da yawa da suke magana akan haka. Ya zo a cikin hadisin Manzon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi cewa: *"Imanin ɗayanku ba ya cika har sai ya sowa ɗan'uwansa abin da yake so wa kansa"*[51]

Kuma Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Wallahi bai yi imani ba,wallahi bai yi imani ba,wallahi bai yi imani ba. Sai Sahabai suka ce waye ya manzon Allah? sai ya ce: wanda maƙwabcinsa bai kuɓuta daga sharin sa ba"*[52]

Yahya ɗan Mu'az Allah ya ƙara masa yadda ya tattaro waɗansu siffofin mumminai a cikin waɗansu rubuce-rubucensa inda yake cewa: Mumini na da yawan jin kunya, kuma da ƙarancin cutarwa, mai yawan alkhairi kuma mai ƙarancin ɓarna, mai gaskiyar zance kuma mai ƙarancin surutu, mai yawan ayyuka kuma mai ƙarancin karkacewa,

[49]Attawba 112
[50]Al-Mu'umin 1-11
[51]Bukhari (1/5,57), Muslim (2/16), Nasa'i (8/115), Tirmidhi (9/319) da Ibn Majah (66)
[52]Bukhari (10/443) da Muslim (2/17)

mai ƙarancin shiga al'amuran da ba su shafe shi ba, mai yawan alheri ga zumunci, mai yawan kyauta, mai nutsuwa, kuma mai godiya, mai yawan yarda da abin da Allah ya ƙuntata na arziƙinsa, mai tausayi, kuma mai kyakkyawar mu'amala da 'yan'uwansa, mai kamewa ga bakinsa, ba mai yawan tsinuwa ba, ko zagi, ko aibatarwa, ko yi da waɗansu, ko yaɗa zance domin husuma, ko yawan gaggawa, ko yawan hasada, ko yawan mugun nufi, ko girman kai, ko jiji da kai, ko mai yawan kwaɗayin duniya, ko mai yawan dogon buri, ko mai yawan yin barci ko rafkana, ko mai yin alheri domin a gani, ko munafunci, ko rowa, mai tattausan al'amari, mai sakin fuska, ba mai ƙasƙankaci ba, kuma ba mai bibiyar sirrin mutane ba, yana so ne domin Allah, yana yarda ne domin Allah, yana fishi ne domin Allah, guzurinsa tsoron Allah, damuwarsa ƙarshen sa, abokin zamansa zikiri (ambaton Allah), masoyin sa Ubangijinsa, ayyukan sa domin lahiran sa.

Fudailu ɗan Iyyad Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: *"Mumini yana shuka dabino kuma yana tsoro kada ta fitar da ƙaya, amma munafiki yana shuka ƙaya ne kuma yana neman ta fitar da kayan marmari"*

Kasan haka ya kai ɗan'uwa domin ka binkici kanka kafin mutuwar ka, ka yi kuka yayin da ka fahimci ɗabi'ar munafukai tare da kai, kuma ka yawaita neman gafara. Dukkan godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin halittu.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Mumini yana aikata alkhairi amma yana tsoron kada sharri ya bayyana cikin wannan aiki.

2- Aljanna ta haramta ga dukkan wanda maƙwabtansa basu kuɓuta daga sharrinsa ba.

3- Almubazzaranci da yawan surutu da gulma da aibata mutane abin zargi ne matuƙa.

4- Munafukai kullun al’amuransu cutarwa ne.

## BABI NA BIYU

## ƊABI'UN MAGABATA WAJEN GABATAR DA AYYUKAN LAHIRA AKAN NA DUNIYA

Daga cikin halayyansu koyaushe shi ne gabatar da ayyukan lahira akan na duniya, don haka kowane ɗayansu ke gabatar da azkar (ayyukan ibadah) bayan sallar asubah gabanin kowane aiki da ke da girma gareshi, Kamar yadda kowane ɗayansu ke gabatar da sallolin dare a cikin dare mai yawan sanyi kan barcinsa cikin mayafi. Akan irin wannan rayuwan ne magabata suka gudanar da rayuwarsu, don haka duk wanda ya wayi gari damuwarsa duniya ce ya fita daga tafarkin su.

Allah maɗaukakin sarki ya ce:

*"Duk wanda yake nufin ayyukansa ga (samun) duniya ne mu zamu gaggautar gare shi abin da muka ga dama, kuma ga wanda muka ga daman (mu ba shi) sa'annan sai mu sanya wutar jahannama ta zame mashigar shi yana mai zama abin zargi da korewa (daga rahamah). Wanda kuwa ya nufi lahira tare da yin ayyukan ta kuma yana mai imani, waɗannan ayyukan su ya zame godaddiya (abin karɓa)'*[53]

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

*"Wanda duk lahira ita ce damuwar sa Allah zai sa wadatarsa a cikin zuciyarsa, kuma ya tattaro masa da kariyarsa, kuma a kawo masa duniya tana ƙasƙantacciya, amma wanda duniya ita ce mafi girman damuwarsa, Allah zai sanya talaucin sa a tsakanin idanuwansa, kuma ya daidaitar da al'amuransa, kuma ba zai zo masa da duniya ba sai abin da ya ƙaddar ta masa'*[54]

---

[53] Isra'i 18-19
[54]Tirmidhi (9/288,289)

Malik ɗan Dinar ya kasance yana cewa; “Duk wanda ya nemi auren duniya za ta nemi ladan ayyukan addinin da ya yi a matsayin sadakinta, kuma ba za ta yarda da komai ba face wannan.

Aliyu Allah ya ƙara masa yarda ya ce: Lahira ta taso tana mai gabatowa kuma duniya ta taso tana nema juyawa da baya, don haka ku kasance ‘ya’yan lahira ka da kusance daga ‘ya’yan duniya. Domin (rayuwarku) a yau yin ayyuka ne babu hisabi amma (rayuwarku) gobe na hisabi ne ba bu aiki.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Fargabatar da ayyukan lahira kafin na duniya.

2- Duk wanda ke nufin samun duniya kawai zai taɓe a duniya da lahira.

3- Duk wanda damuwarsa lahira ne Allah zai isar masa ga buƙatunsa na duniya da lahira.

4- Lada da sakamakon addini a lahira ake samun su cikakke.

5- Mutum zai fuskanci hisabin ayyukansa ne kawai a lahira.

## BABI NA UKU

## ƊABI'UN MAGABATA WAJEN YAWAN AMBATON ALLAH DA SALATIN ANNABI TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI A DUK INDA SUKA ZAUNA.

Daga cikin halayyarsu akwai rashin rafkanarsu daga Ambato da tunanin Allah da kuma yin salati ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi a kowane wurin zama daga wuraren zamansu. Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Lallai ambaton Allah shi ne mafi girma"*[55]

Kuma Allah ya ce: *"Ku saurara da ambaton Allah ne kawai zukata suke natsuwa"*[56]

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Misalin wanda yake ambaton Allah, Ubangijinsa, da wanda kuma ba ya yi kamar misalin rayyaye da matace ne"*[57]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Babu waɗansu mutane da za su zauna a wani wuri, sannan su tashi ba su ambaci Allah ba face sun tashi kamar mushen jaki kuma daga ƙarshe ya zama abin nadama a gare su ranar alƙiyama"*[58]

Hasanul Basari Allah ya yarda da shi ya kasance yana cewa: *"Haƙiƙa Allah ya sauƙaƙa a kanmu a cewarsa: ku ambace Ni sai nima in ambace ku"*

Allah a wannan umarnin bai keɓantar da wani wuri ba, da ko ya keɓantar da wani wuri da cewa anan za a ambace shi, da ya zama wajibi akan musu wurin, ko da kowa zai ɗauke mu tafiyar shekara ɗari ne. Kamar yadda ya umarci mutane da kiran sa zuwa ka'abah, lallai godiya da kyautatawa duk sun tabbata gare shi.

---

[55]Ankabut 45
[56]Ra'ad aya 28
[57]Bukhari (11/208) da Muslim (6/68)
[58]Abu-Dawud (4834) Al-Adab, Hakim (1/492), Abu Nu'aim (7/207) da Ahmad (2/389)

Fudailu ɗan Iyyad ya kasance yana cewa: *"Idan kuka ambaci waɗansu a wuraren zamanku to ku gaggauta ambaton Allah, domin ambaton Allah magani ne daga cutar ambaton waɗansu"*

Abu Malik ya kasance idan ya ambaci Allah Maɗaukakin sarki sai farin ciki da jin daɗi ya shige shi kuma sai ya ce: Ni ambaton Allah kawai shi ne jin daɗi na domin Allah maɗaukakin sarki yana cewa: *"Ku ambace Ni zan ambace ku"*

Ya kasance idan ya biyo wata hanya bai ambaci Allah ba a cikinta sai ya koma ya ambaci Allah a cikinta ko da sau ɗaya ne, Sai ya ce *"Ni ina son wurare su ba da shaida akan haka ranar ƙiyama.''*

Yahaya ɗan Mu'az y ace Maɗaukakin sarki ya kasance yana cewa: ku sabantawa zukatanku da ambaton Allah domin tana (zuciya) da saurin rafkana.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1. Ambaton mutane ba da alheri ba a wuraren zama zunubi ne babba.
2. Babbar hasara ce a zauna a wani wuri ba tare da ambaton Allah ba.
3. Duk umarnin Allah na ayi ko a bari sauƙi ne kuma amfani ne ga mutane.
4. Ana kiwatar zuciya ne da yawan ambaton Allah.
5. Zuciyar da bata luzumci ambaton Allah tana komawa mazaunin shaiɗanu.

# BABI NA HUDU

## ƊABI'UN MAGABATA WAJEN YAWAN KUKA DOMIN SAKACINSU A KAN HAKKIN ALLAH

Daga cikin halayensu sassaucin zuciyoyinsu, da yawan kukan su domin fahimtar sakacinsu a cikin haƙƙoƙin Allah maɗaukaki, don ko Allah zai jikansu Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Da kun san abin da na sani ? da kun yi dariya kaɗan kun yi kuka da yawa"*[59]

Wannan bayanin da Annabi ya faɗi sai ya sanya sahabbai suka rufe fuskokkin su suna ta gurnanin kuka. Ali ɗan Abi Talib Allah ya ƙara masa yarda ya ce:

*"Na ga sahabban Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ban ga waɗanda suka yi kama da su a yau ba, sun kasance suna wayar gari bususu kawunansu fatsi-fatsi don ƙura, tsakanin idanuwansu kamar misalin 'yan Mahaya masu ta'aziyya, domin sun kwana sujjada da tsayuwa, suna hutu ne a tsakanin fuskokinsu da ƙafafuwansu, yayin da suka wayi gari sai su zarce da ibadah, kamar yadda bishiya ke karkaɗawa lokacin iska, idanuwansu suna kwarayar da hawaye. Na rantse da Allah kai ka ce ni ina cikin mutanen da a yanzu sun kwana a rafkane"*

Umar ɗan kaɗɗabi Allah ya ƙara masa yarda ya kasance a fuskarsa akwai waɗansu baƙaƙen zane guda biyu saboda yawan kuka.

Abdullahi ɗan Abbas Allah ya ƙara masa yadda ya kasance a ƙarkashin idanuwansa akwai kamar tsohowar hancin takalmi saboda yawan kuka.

Ka'abul Akbar Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa:

---

[59]Bukhari (11/319) A-Rikak da Tirmidhi (9/194) Az-Zuhdu

*Inyi kuka saboda tsoron Allah har ɗigon hawaye ɗaya ya zubo mini shi yafi soyuwa a gareni da inyi sadaka da zinare mai girman ƙaton dutse ina mai kakkausar zuciya.*

Ali ɗan Abi Talib Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: *"Daga cikin alamar managartan mutane shi ne fatsi-fatsin launuka, da raunan nan idanu mai cike da hawaye, da busasshiyar lebban saboda yawan raya dare da kuka da yunwa.*

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA:-

1- Yawan kuka domin Allah yana gyara zukata.

2- Yin sadaka tare da ƙeƙashewar zuciya baya amfanarwa.

3- Yawaita dariya na aibatar da zuciya daga barin tsoron Allah.

4- Sanin tarihin mutane managarta na taimako wajen gyaran imani.

Daga cikin halayyarsu yawan zato da jingina halaka ga kawunansu, saboda ganin gajiyawarsu wajen bin umarnin addini ballantana yayin da suka yi la'akari da shigarsu cikin saɓawa shari'ah.

Sun kasance abin ƙauna daga Allah wanda ba makawa shi ne yafiyarsa a garesu. Yadda sha'anin yake ga zaton kowane ɗayansu cewa Allah, yana iya kama shi daga dukkan abu ƙarami marar muhimmanci, domin sanin hakan ko ya sauƙaƙawa kansa a lokacin tsayuwarsa ranan Kiyama.

Don duk wanda bai yiwa kansa hisabi ba a duniya lallai zai tsawaita wa kansa tsayuwa a ranan lahira. Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Ya ku waɗanda kuka yi imani kuji tsoron Allah kowace rai ta dubi abin da ta gabatar gobe (lahira)"*[60]

Umar Allah ya ƙara masa yarda ya ce: *''ku yi wa kawunan ku hisabi kafin a yi muku hisabi, ku auna ayyukanku kafin a auna muku, ku yi shiri saboda fuskantar mafi girman al'amari. Domin a wannan ranar za a bijiro da ku ba ku da wani abin ɓoyewa.''*

Abdurrahman ɗan Hurmuz Al-A'araj Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: *''ku binciki kanku a cikin abubuwan da ku ke yi munana, domin kowane ɗayan ku za a tashe shi ne gobe (lahira) da ma'abota ayyukansa.''*

Duk wanda ya faɗa cikin kowane saɓo yana da sakamako na irin dukkan masu laifuffukan. Kuma ya kasance sau da yawa yakan yi zargi tare da tuhumar kansa, sai

[60](Hashr aya 18)

ya cewa kansa: yayin da mai kira zai yi kira ranar ƙiyama da cewa ya ku ma'abota laifuffuka ka da ku tashi. Sai A'araj (shi kansa) ya ce ku tashi tare da su.

Sannan kuma mai kira ya koma kiran waɗansu irin ma'abota laifuffuka da su tashi sai A'raj ya ce ki kuma tashi tare da su, haka za a ci gaba da ambaton laifuffuka daban-daban a kowani laifi sai A'raj ya ce kin tashi a cikin su. Don haka nake ganin A'raj kana cikin kowane laifi.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA:-

1- Jin tsoron dukkanin zunubai ƙanana da manya.
2- Gujewa daga wuraren saɓawa Allah tare da gujewa daga mai saɓawa Allah.
3- Yi wa kai hisabin ayyuka na daga cikin cikan hankali.
4- Rashin ganin tsarkakar kai na taimako wajen ƙara tsoron Allah.
5- Tuna ranan ƙiyama da rana ce ta tonon asiri.

Daga cikin halayyarsu rashin damuwa da gine-ginen gidaje da makamartansu. Har idan ya zama babu makawa ga ɗayansu sai ya gina gida to zai taƙaitu ne kawai ga buƙatuwar gida ba tare da ya damu da ƙawace-ƙawace ba.

Mafi yawanci dalilin da ke sa yin haka, sai domin rashin samun cikakken halal da zai yi aikin, kuma da rashin dogon buri. Domin gajeruwar burin su ba zai bari su shiga ƙawace-ƙawace ko gine-gine barkatai.

An karɓo daga Anas Allah ya ƙara masa yadda ya ce: Manzon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya yi mana wani zane ya ce: wannan shi ne mutum, sai ya yi wani zanen a gefen shi, sai ya ce: wannan shi ne ajalinsa, sai kuma ya yi wani zanen amma mai nisa daga gare shi, sai ya ce: wannan shi ne gurace-gurace yana cikin halin haka sai na kusa ya zo masa.[61]

Wani daga cikin magabata ya wuce wani mutum da ya gina gida kuma ya kyautata gidan sai ya rera waƙe yana cewa: ka gina ginin masu dawwama domin ai tsayuwarka a ciki da zaka hankalta na lokaci ne ɗan kaɗan.

Haƙiƙa ya kasance wadatuwa cikin inuwan Araaka (shingen itace), ga duk wanda yini ɗaya, ya isa ya hukuntar da tafiyarsa (barin duniya). Waɗansu daga cikin magabata sun kasance suna aibata talaka yayin da suka gan shi yana gina gida sai su ce da shi: "lallai abin da kake kashewa na dukiya a wajen gina irin wannan gidan ba za ka riska zama cikinta ba. Wani mutum ya gargaɗi wani daga cikin abokanansa da ya gina gida ya kashe masa maƙudan kuɗi, sai ya ce: da ka nema inda zaka zauna wajen haya da ya

[61]Bukhari (11/235,236)

ishe ka ɗaya bisa goman abin da ka kashe wajen wannan ginin. Haƙiƙa magabata sun bi matakai a wajen rashin kwaɗayi da dogon buri

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA:-

1- Ajalin mutum na kusa da shi amma dogon buri ke mantar da shi.

2- Halarcin gina gida mai kyau ba tare da almabuzaranci da taƙama ko alfahari ba.

3- Auna komai da amfaninsa a lahira sannan da fifita shi akan buƙatun duniya.

4- Yawan tuna mutuwa na ƙaiyaje dogon buri.

## BABI NA BAKWAI

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN RASHIN GANIN KIMAR DUNIYA DA GUDUNTA

Daga cikin halayyarsu rashin ɗaukar duniya da muhimmanci tare da kuma guje mata. Saboda ƙoƙarin bin umarnin Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi a cewar sa: *''Duniya ba komai ba ce game da lahira face kwatankwacin abin da ke ragewa na ruwa akan ɗan'yatsan ɗayanku ya yin da ya tsoma cikin teku ya fitar da shi*[62]*''.*

Kuma Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Da duniya ta kai darajar fiffiken sauro a wurin Allah da kafiri bai sha ko da maƙwarwa ɗaya ta ruwa ba'*[63]

Malik ɗan Dinar ya kasance yana cewa: ku kiyayi sihiri, ma'ana duniya, mai sihirtar da zukatan malamai kuma ta shagaltar da su daga barin Allah. Wannan sihirin ita ce mafi munin daga sihirin Haruta da Maruta, domin su sihirin su ya taƙaita ga raba tsakanin mutum da matarsa ne, ita kuwa duniya sihirin ta na raba tsakanin bawa da mahalicin sa ne.

Hasanul Basari ya kasance yana cewa: Haƙiƙa mun riski waɗansu mutane suna ganin duniya a gurin su kamar kayan ajiya ce da za su mayar ga masu shi, don haka ba su da wani iko da ita. Domin haka su ka koma zuwa lahira babu wani nauyi a kansu.

Abdullahi ɗan Mubarak ya kasance yana cewa: Duniya kurkukun Mumini ce, don haka mafi girman ayyukan wanda ke cikin kurkuku haƙuri da rashin fishi, bai zame ba ga Mumini wata daula a duniya ba domin shi daular sa tana tafe ne gobe (lahira).

[62]Muslim (18/93) da Tirmidhi (9/199) da Ibn Majah (410)
[63]Tirmidhi (9/198)

Abin da yake nufi da shi, shi ne Mumini baya nufin duniya da ayyukansa, kamar yadda Allah ya faɗa: *"Wancan gidan lahira mun sanya ta ga waɗanda basa nufin ɗaukaka ko aikata barna acikin duniya, lallai ƙarshe mafi kyau na ga masu tsoron Allah"*[64]

Sai dai abin la'akari da shi, shi ne Allah Maɗaukakin sarki yanaɗaukaka Mumini cikin duniya da lahira, sai ya sami girman duniya kamar yadda zai sami girman lahira da ɗaukakanta.Waɗansu daga cikin magabata kance: Idan ka nufin samun kusanci da Allah (SWT) sai ka sanya Katanga karfe tsakanin ka da sha'awowi.

WANANAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA :-

1- Bin sha'awe-sha'awen zuciya shamaki ne tsakanin bawa da mahaliccin sa.

2- Duniya mayaudariya ce don haka ya zama dole ruƙo da addini domin kuɓuta.

3- Yin ibadah na buƙata haƙuri, natsuwa da rashin fishi domin kai wa ga nasara.

4- Dukkan girma da ɗaukaka na Allah ne.

[64](Al-Kasas 83).

## BABI NA TAKWAS

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN RASHIN ƁARNA A KAN ABIN DA YAKE HALAL NE

Daga cikin halayyarsu rashin ɓarnarsu acikin abubuwan halal idan suka same shi. Saboda ita halal takan zo ne gwargwado a kowane zamani da bambance-bambance a tsakanin mutane.

Sun kasance suna gabatar da dirhami da suka nema na halal a kan kowane abu mai muhimmanci a gare su. Saboda su suna da tabbacin zama 'ya'yan lahira ne, masu aiki domin lahira kawai, don haka ba su yarda da wani abu na haram ko shubuha ta auka ga hannayensu. Domin duk wanda ya ci daga haram ayyukan haram za su keto daga gare shi, kamar wanda ya ci daga shubuha ma zai karkatu ga aikata shubuha. Duk kuwa wanda ya ci haram yana son ya yi wa Allah biyayya ba zai iya ba. Wataƙila shi ya sa Allah ya daidai ta Annabawa da muminai a cikin umarni da cin mai daɗi cikin halal ga kowane mutum. Manzon Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

*"Lallai Allah Maɗaukakin sarki tsarkakke ne baya karɓa kowane aiki sai mai tsarki, kuma Allah ya umarci muminai da abin da ya umarci manzani da shi, ya ce: "Ku ci daga tsarkakan abubuwa kuma ku yi aiki nagari"[65] Kuma ya ce ya ku wanɗanda ku ka yi imani ku ci daga cikin tsarkakan abubuwan da muka azurta ku da shi sannan kuma ku godewa Allah in kun kasance shi ka ɗai ku ke bautawa"[66]*

Don haka cin halal mai daɗi ga mutum shi ne mafi girman abin da ke taimako a wajen aikata ayyuka managarta, kuma shi ne sharaɗin karɓar adduo'i. Yunus ɗan Ubaid

[65]Al-mu'umininun aya 51
[66]"Bukhari (172) Muslim (7/100) da Tirmidhi (11/110)

Allah ya yarda da shi ya kasance yana cewa: mafi wahalar dirhami (kuɗi) a yanzu shi ne na halal da zamu same shi da mun warkar da marasa lafiyarmu da shi.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA;-

1- Cin haram na haifar da rashin iya yin ibada karɓaɓɓiya.
2- Amfani da halal samun waraka ne daga cututtuka da fitintinu.
3- Shubuha na daga cikin abubuwa masu gaggawar halakar da mutum.
4- Mumini sai ya yi taka tsantsan wajen neman halal.

BABI NA TARA

ƊABI'UN MAGABATA WAJEN RASHIN GANIN YAWAN AYYUKANSU NA GARI

Daga cikin halayyarsu ita ce ganin ƙarantar ayyukansu na alheri dangantaka da abubuwan da suka samar ita, wanda ya kamata ya kasantar da su cikin Ibadar da Allah ya ɗora wa Mutum da Aljani. Don haka suka kasance ba sa ganin cewa su sun tsayu da aiki mafi ƙanƙanta na daga haƙƙoƙin Allah.

Waɗansunsu kasance, haƙƙin Allah shi ne mafi nauyin abin da bayin Allah ya kamace su tsayu akai, domin ni'imomin Allah sun yawaitu ga bayin Allah da su kidaya ko su iyakance su, sai dai kawai su zama cikin tuba safiya da yammaci.

Annabi ya kasance yana yin Sallah har ƙwaurukansa su yi rauni kuma dugadugansa su kumbura. Idan aka ce da shi kana aikata haka ga kanka bayan an gafarta maka zunubin abin da ka gabatar da wanda ka jinkirtar, sai ya ce: "bai zama ya da ce in kasance bawa mai godiya ba?"

Sabitul Bunnani ya kasance yana cewa: Ya ubangiji idan zaka ba da izini ga wani da ya yi Sallah a cikin ƙabarinsa ka bani wannan damar.

Waɗansu sun shiga wajen Junaidu a lokacin yana Sallah kuma yana motsin kusa da ƙarshe na mutuwa sai aka ce masa yanzu ne fa? Sai ya ce yanzu za a nannaɗe littafin ayyuka na.

Ɗayansu ya kan yi begen zuwan dare, domin a lokacin yake fuskantar daren da keɓanta domin ganawa da Ubangijinsa. Ya kan damu da yinin idan ta fuskanto saboda tsoron mutane ka da su shagaltar da shi daga barin bautan Ubangijinsa. Sun kasance

sun kai matuƙa wajen yin Ibadah, ta yadda da za a cewa ɗayansu gobe ne ranar ƙiyama da ba abin da zai iya ƙarawa na Ibadah.

An karɓo daga Muhmmad ɗan Abi Umairah ɗaya daga cikin sahababan Annabi ya ce Manzo Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce da za a ce mutum zai kife (yana mai sujjada) a kan fuskan sa tun daga ran da aka haife shi zuwa mutuwarsa, ya tsufa yana mai da'a ga Allah da sai ya raina aikinsa a ranan nan (ƙiyama), da sai ya guraci ya ƙara kamar yadda yake neman ƙari na lada da sakamako"[67]

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA:-

1. Lura da Ni'imar da Allah ya yi maka domin ƙarin yawan Ibadunka.
2. Ganin ƙarancin ibadarka kullum domin ka ƙara zabura.
3. Yin ibada a kowane lokaci kamar lokacin mutuwanka ya yi.
4. Karin ibada nuna godiya ne ga ni'imomin Allah.

[67]Ahmad (4/185) ya ruwaito shi.

## BABI NA GOMA

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN KWAƊAYIN ƊORA MUTANE A KAN HANYAR ALHERI DA TSORON ƁACIN AYYUKANSU.

Daga cikin halayyarsu yawan tsoron shigar aibi cikin ilimi da ayyukan ibadarsu, da kuma ayyukansu na shiryar da al'umma zuwa ga abin da ya zama kyautatuwar duniyarsu da lahirarsu.

Ba ma za ka yi zaton akwai wani daga cikinsu da ke da ƙaunar jagorancin wani abu daga cikin al'amuran duniya. Sun kasance suna ƙyamar yin fatawa saboda mai yin fatawa na shiga tsakanin Allah da bayinsa ne. Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Ka da ku ce ga abubuwan da harsunanku ke siffatawa na ƙarya cewa kaza halal ne kaza kuma haram ne domin ƙirƙirar ƙarya ga Allah, lallai waɗanda ke ƙirƙirar ƙarya ga Allah ba za su rabauta ba"*[68]

Abdurrahman ɗan Abi Lailah ya ce: *"Na riski sahabbai ɗari da ashirin (120) babu wani daga cikinsu mai ba da labari (na Hadisi) face sai ya guraci ɗan'uwansa ya isar masa wajen ba da Hadisai, haka kuma babu mai fatawa face sai ya guraci ɗan'uwansa ya isar masa wajen ba da fatawa"*

Fudail ɗan Iyyad ya kasance yana cewa: In rabawa mutane kuɗi (dinare) ya fi soyuwa a gare ni da in gaya musu Hadisi, hakan kuma shi ya fi sauƙi ga rayuwata.

Muntane sun nemi daga Sufyan ɗan Uyayna da ya zauna yana karantar da su Hadisi amma sai ya ƙi, sannan ya ce ni ba wanda ya cancanta ne da ya karantar da ku Hadisi ba, kuma ku ba waɗanda suka cancanta ne ga saurare ba, babu abin da yake misali na

---

[68](Nah'li aya 116)

da misalin ku face sai kamar yadda mai zance ya ce: “da asirinsu ya tonu sai suka daidaitu”

Abu Muslimul Khaulani Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: Da yawa daga cikin mutane, waɗansu mutane ke rayuwa da ilimin su, yana kuma kashe abin da ke cikin zukatan na girman kai da taƙama.

Abu Hazim Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: Malaman zamaninmu sun yarda da zantuka amma sun bar aiki, su kuwa magabata suna yin aiki ne ba tare da zance ba, daga nan waɗanda suka biyo bayansu sai suka zama masu yin aiki da zance, sannan waɗanda suka biyo bayan na gaban su sai suka zama suna zance basa aiki. Da sannu zamani zai zo mutanen za su bar zance kuma subar yin aiki.

Abdurrahmanus Sulami Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: Mun riski mutane suna neman ilmin Kur’ani da ayoyi goma-goma, basa wuce ayoyi goma sai bayan sun yi aiki da karantarwarsu.

Abdullahi ɗan Mubarak ya ruwaito daga Muhammad ɗan Ziyad wanda ya ce: Na ga Abu Umamah ya zo wurin wani mutum a masallaci yamyi sujjada yana ta kuka kuma yana kiran Ubangijinsa. Sai Abu Umaamah ya ce masa kai da a gidanka ne ya kamata. An ce wa Sha’abi Allah ya ƙara masa yadda wata rana da ya wuce sai aka ce da shi ka yi mana fatawa ya kai wannan malamin, sai ya ce, ka da ku cewa kamata malami, domin wanda yake malami shi ne wanda gaɓoɓinsa suka tsintsinke saboda tsoron Allah.

Sufyanut Thauri Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: wanda iliminsa ya sa shi kuka shi ne malami. Allah maɗaukakin sarki ya ce: *“Lallai wanɗanda aka ba su*

*ilimi kafin su idan aka karanta masu ayoyinsa suna faɗuwa da kuncinsu suna masu sujada"*[69]

Kuma Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Idan aka karanta musu ayoyin Allah mai Rahma sai su faɗi suna masu sujjada da kuka"*[70]

Ya kai ɗan'uwa ka lura da zuciyarka shin ka cika haƙƙoƙin iliminka da ayyukanka kamar yadda waɗancan suka cika nasu ko kai dangantakarka da su ta nisanta ne? don haka ka yawaita yin istigfari dare da rana.

WANNAN BABI YANA KOYYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA;-

1. Ma'anar ilimi shi ne aiki da shi kamar yadda addini ta shar'anta.
2. Gujewa bayanin addini yayin da akwai waɗanda suka fika.
3. Haramcin karantarwa ba tare da ilmi ba.
4. Rashin gaggawa wajen neman ilimi.
5. Fahimtar ilimi yafi tarin ilimi mai yawa.

---

[69](Al-isra'i aya 107)
[70](Maryam aya 58).

# FASALI NA HUDU

## BABI NA ƊAYA

## HALAYYAR MAGABATA DANGANE DA TAMBAYAR HALAYEN DA 'YAN'UWANSU SUKE CIKI

Daga cikin halayyarsu yawaita neman labarinsu game da halin da abokanansu ke ciki, domin su ɗebe musu kewa na basu abin da suke buƙata na abinci, tufafi, kuɗi ko biya musu bashi, domin ɗauke musu damuwa.

Irin waɗannan ɗabi'un ya zama masu yin shi kamar baƙi ne a wannan zamanin, domin mutane a yau sun saɓama waɗannan ɗabi'un. Akan iya samun wani ya ce ma abokin sa ya ya ku ke? Sai ya ce masa lafiya tare da ɓoye al'amarinsa domin ya sani abokinsa baya da tunaninsa.

Domin tambayarsa ya ya ku ke, na al'ada ne wanda baya tattare da biyan buƙata. Kamar yadda yake aukuwa sau da yawa mai wucewa yake cewa abokanansa ya ya ku ke? Bai da buƙatuwar sauraren amsa, shi ma wanda yake tambaya ba ya jiran har sai an ba shi amsa.

Shi ma wanda ake tambayar bai ɗorawa kansa sai ya buɗe baki domin ya amsa ba. Waɗansun su sun ce idan ba bu wanda ke da niyyan ɗebe kewa ga ɗan'uwansa, ko ɗauke masa damuwarsa, ko yi masa addu'a to kada ya ce masa ya ya ka ke?

Domin haka kamar munafunci ne su magabata sun kasance sukan tambayi junansu halin da suke ciki domin su faɗakar da wanda ya gaffala da yin godiya ga Allah don ya gode, da haka alheri sai ya sadu das hi da kuma su.

An ce wa Abubakar ɗan Siddiƙ ya ya ka wayi gari? Sai ya ce, na wayi gari bawa ƙasƙantacce ga Ubangiji maɗaukaki, kuma na wayi gari ina mai aiki da umarninsa.

An ce wa Imamus Shafi'i ya ka wayi gari? Sai ya ce "Na wayi gari ina mai cin arziƙin Ubangijina kuma ban zama mai gode masa ba. An ce wa Malik ɗan Dinar ya ka wayi gari? Sai ya ce na wayi gari cikin rayuwa mai ragewa kuma zunubi mai ƙaruwa.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA:

1. Ɗabi'ar muminai ita ce bincikan halin 'yan'uwansu da gaskiya domin ba su gudunmuwa.
2. Duk godiyar da bawa zai yi wa Allah a kai ba zai iya biyan Sa ni'imar da ya yi masa ba.
3. Ana son bawa ya yawaita damuwa ga zunubansa da kuma ƙarancin ayyukansa alheri.

Daga cikin halayyarsu rashin gafala daga gaban Shaiɗan da kuma ƙoƙarin gane irin ƙulle-ƙullensa da hare-harensa. Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Lallai shiɗan maƙiyi ne agare ku, don haka sai ku riƙe shi maƙiyi, abin da shaiɗan ya ke yi kawai shi ne kiran mabiyansa da su kasance 'yan wuta"*[71]

Wannan ɗabi'ar da yawa mutane sun gafala daga gareta kamar yadda shaiɗan ba ya gaffala daga gare su, domin haka ya kamace kowanne mutum da ka da ya mance da shaiɗan, don yana nan a madakata cike da kwaɗayin ya jefa bawa cikin fishin Allah.

Manzo Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Lallai Iblis yana ɗora gadansa akan teku sai ya aika da waɗanda ya ribata da rundunoninsa, mafi girman matsayi a wurinsa, shi ne wanda yafi zama fitina ga mutane"*[72]

Fudail ɗan Iyyad Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ya yin da Iblis ya samu rinjaye akan mutum bisa ɗayan abubuwa ukun sai ya ce: ba na ƙara neman wani abu daga gare shi. Abubuwan sune: mutum ya rinƙa mamakin kansa, ganin yawan aikinsa, da kuma mantuwarsa ga zunubansa.

Wahab ɗan Munabba Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: kashedinku da yin ƙiyayya da shaiɗan a bayyane sannan ku yi masa biyayya a halin ɓoye, domin duk wanda ya kwana yana mai saɓo shi kuma shaiɗan a dalilin haka zai kwana kwanan ango.

Ya kai ɗan'uwa ka wa'azantu ga kanka, ahir ɗinka! Zaton shaiɗan ya yanke daga gareka don ka ga ka jiɓinci ibadunka, a'a ka zama mai lura a ciki, kuma kana dukkan bincike, sai kaga rabon shaiɗan don haka sai ka yawaita neman tuba.

---

[71] (Fadir 6).
[72]Muslim (2813)(67)

An karɓo daga Hassan ya ce: idan shaiɗan ya yi kallo gareka sai ya ganka ka luzumci biyayya (ɗa'a) ga Allah, sai ya ɗora nemanka lokaci bayan lokaci, ya yin da ya ga ka dai luzumta cikin ibadah lokaci mai tsawo sai ya ƙyale ka, amma idan ya ga a wani lokaci kana kaucewa sai ya yi kwaɗayin yin nasara a kanka.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA:

1- Haɗarin ƙiyayya ga shaiɗan a baki amma biyayya gareshi a aikace .

2- Yawaita tunani daga makirce-makircen shaiɗan da ɗaukan mataki a kai.

3- Luzumtuwa cikin Ibadah yana kariya daga shaiɗan.

4- Gujewa daga mamakin kai, ko ganin yawan Ibadarka, da kuma mantuwa daga zunuban ka.

BABI NA UKU

# HALAYYAR MAGABATA WAJEN NUNA GAZAWARSU A WAJEN GODEWA NI'IMAR ALLAH

Daga cikin halayyarsu akwai shaidawa ga kansu da cewa ba su yi aiki daidai da ƙwayar zarra guda na godiya ga Ubangijinsu, wannan kuwa ya kasance ne domin suna ganin dukkan abin da za su gode masa da shi ai daga cikin tarin ni'imarsa ne a kansu, don haka ba za a iya kawar da ni'imarsa ba a kansu, kuma baya inganta wani ya ƙalubalance ta.

Bakar ɗan Abdullah Al-Muzni Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: Idan Bawa ya ce godiya ta tabbata ga Allah (Alhamdulillah) face akwai wani dalilin da zai kuma wajabta masa wata godiyar ga Allah, domin wannan (samun damar) wata ni'ima ce dake buƙatar godiya ta daban.

Wahab ɗan Munabbah Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: idan ya kasance abin da ka ke godewa Allah da shi, ni'ima ce daga gareshi akan ka, cikin ni'imominsa Maɗaukakin sarki, to mene ne gaskiyar godiyar bayan haka? Ita godiya ashe faɗin bakinka ne da ni'imarsa a kanka, don haka kai ba zaka iya iyakance yabo a gareshi ba.

Sahal At-Tustari Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: yin godiya ga Allah Maɗaukakin sarki da cewa kai ba zaka saɓama masa ba saboda ni'imarsa da ya yi a kanka, domin gaɓoɓinka dukkaninsu na daga cikin ni'imarsa a gareka don haka ba zaka saɓa masa da wani daga cikinsu ba.

Mujahid da Mak'hul Allah ya ƙara musu yarda sun kasance suna cewa game da faɗin

Allah maɗaukakin sarki: “Sannan tabbas za a tambaye ku a wannan rana game da ni’ima”[73]

Suka ce shi ne abubuwan sha mai sanyi, da inuwan gidaje, da ƙoshin cikkuna, da dai-daituwan halitta da kuma daɗaɗan bacci.

Sufiyanut Thauri Allah ya ƙara masa yarda ya kasance idan wani da ga cikin ‘yan sanda ya wuce ta gabanss sai ya faɗi yana mai sujjada ga Allah Maɗaukakin sarki yana cewa: “Na godewa Allah da bai sa na zama ɗan sanda ba ko mai amsar kuɗin shiga ga ƙasa ba. Sannan sai ya cewa abokanansa: akwai wanda zai zo ya wuce ta gabanku wanda aka jarabce shi ana biyansa ne ta jarabtarsa, saboda haka ku sai ku roƙi Ubangijinku rangwame. Hakanan, irin waɗannan azzaluman waɗanda ke ɗaukar alhaki da jarabawarsu basa rokon Allah yafiya.

Hassanul Basari Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa game da zancen Allah: *“Lallai mutum game da Ubangijinsa mai yawan tsaurin kai ne”*[74]

Ya ce abin da ake nufi shi ne mutum kan ƙidaya musibu da suka same shi amma ya kan manta da ni’ima da aka yi masa.

Aunu ɗan Abdurrahman Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa game da faɗin Allah madukakin sarki: *“Suna sanin ni’imar Allah sannan sai su musanta”*[75]
Ya ce abinda ake nufi suna ganin ni’imomi daga Allah amma sai su jingina su zuwa ga wata halitta, suna masu rafkana daga barin Allah Maɗaukakin sarki, suna cewa ba don wane ba! da kaza da kaza bai same mu ba.

---

[73](At-Takasur aya 8)
[74](Al-Adiyat aya 6).
[75]“(An-nahl aya 83)

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Ni'imomin Allah sun yawaita ga mutum har ba zai iya iyakance su ba.

2- Ya wajabta da a godewa Allah saboda da ni'imomin sa.

3- Dukkan ni'imomi da Allah ya yi wa mutum zai tambaye shi yadda ya aiwatar da su.

4- Godiya da bautar Allah saboda ni'imarsa sababi ne na ƙaruwarta.

5- Zalunci ne jingina wani samun alheri ga wanin Allah.

BABI NA HUDU

HALAYYAR MAGABATA WAJEN TAKATSANTSAN A KAN TSORON ALLAH

Daga cikin halayyarsu akwai tsananin tsantseninsu ga tsoron Allah da kuma kaffa-kaffan kowanensu wajen jinginawa kansa tsoron Allah. Allah maɗaukakin sarki ya ce:

*"Kada ku tsarkake kawunanku, Allah shi ne mafi sani ga masu taƙawa"*[76]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Tsoron Allah a nan yake" sai ya nuna ƙirjinsa Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi*[77]

Umar ɗan Abdulaziz ya kasance yana cewa: Ɗayan ku baya isa matsayin mai tsoron Allah har sai ya kasance ba shi da wani zance ko aiki wanda zai kunyata da shi a duniya da lahira. Wata rana wani mutum ya ce masa: yaushe ne mutum zai kai ƙololuwar tsoron Allah? Sai ya ce: idan mutum ya fito da dukkan abin da ke cikin zuciyarsa na tunani ya sa su a faifai sannan ya kewaya kasuwa bai ji kunyar komai ba a cikin su.

Ya kuma kasance yana cewa, "Alamar mai tsoron Allah shi ne ya sama zancensa linzami kamar yadda mai aikin hajji yake kamewa lokacin da ya shiga cikin Ihrami. Yana buƙatuwa ga wanda yake yawan tsoron Allah ya zama masani ga shari'o'in addini dukkaninta, in ba haka ba sai ya fita daga ƙa'idojin tsoron Allah ba tare da ya sani ba.

Abu Darda'i ya kasance yana cewa: "Yana daga cikar tsoron Allah Bawa ya tsoraci Ubangijinsa har cikin kowani ƙaramin al'amari.

Haƙiƙa an tambayi Abu Hurairah game da tsoron Allah sai ya ce: "tsoron Allah hanya ce mai ƙaya, don haka matafiyi a kanta na da buƙatar haƙuri mai tsanani.

---

76

77 Muslim (16/120,121), Tirmidhi (8/115) da Ahmad (2/277)

Sufiyanut Thauri ya kasance yana cewa: mun riski mutane waɗanda suke son wanda duk ya ce wa waninsu ka ji tsoron Allah, amma a yanzu sun zamo suna cikin damuwa wajen samun haka.

Wani mutum ya ce wa Fudail ɗan Iyyad wani gari ka ke so in zauna a ciki? Sai ya ce: ka zama baka da dangantaka da kowane gari, kai dai fiyayyen gari a gareka shi ne garin da ya ɗauke ka zuwa ga tsoron Allah. Ka binciki kan ka yakai ɗan'uwa shin kana jin tsoron Allah kamar yadda waɗancan magabatan suke, ko ka gaza ga kaiwa kamarsu, ka nemi gafarar Ubangijinka. Godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin hallitu.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Mutum bai isa da ya tsarkake kansa ko waninsa ba domin Allah shi ya san mai tsoronsa domin a zuciya ta ke.

2- Kyakyawan garin musulmi kuma abin alfaharinsa, shi ne garin da ya ke taimakonsa wajen tsoron Allah.

3- Kiyaye zantuka na kai wa ga samun tsoron Allah.

4- Yin wa'azi da tsoron Allah ga mutum na nuna matuƙar soyayya don Allah.

## BABI NA BIYAR

## NA DAGA ƊABI'UN MAGABATA ƁOYE LAIFIN 'YAN'UWANSU

Daga cikin halayyarsu yawaita ɓoye asirin musulmai, da kuma tsananin bincikar zuciyoyinsu game da tsantseni. Sun kasance ba sa ƙaunar bayyanar da ɓoyayyen aibin waninsu, kuma sun kasance suna wa kawunansu bincike game da zantuka da ayyuka da abinci da abubuwan shansu, sukan kuma bincike dukkanin gaɓɓansu musamman harsunansu, da farjinsu, da idanuwansu a cikin aukawarsu ga abubuwan da Allah ya haramta a garesu.

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

*"Ka kiyaye abubuwan da aka haramta, sai ka kasance wanda yafi kowa bautar (Allah). Ka kuma yarda da abin da Allah ya baka sai ka kasance mafi wadatuwar mutane, ka kyautata ga maƙwabcinka sai ka kasance mai imani, ka so wa mutane abin da ka ke so wa kanka sai ka kasance musulimi, ka da kuma ka yawaita dariya domin dariya na kashe zuciya"*[78]

Yunus ɗan Ubaid Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: "Haƙiƙanin tsantseni shi ne fita daga dukkan shubuha (rikitattun al'amura a addini) da kuma bincikar kai a kowane lokaci, saboda duk wanda bai zame haka ba shi ba mai tsan-tseni ba ne.

Sashensu ya kasance yana cewa " ka da ka wulaƙantar da yin tsantseni cikin komai ƙanƙantar abu, domin wulaƙantarwa na da tsani na kai wa ga barin yin tsantseni ga mafiya yawan al'amura.

---

[78]Tirmidhi (9/183,184), Ahmad (2/3/10) da Ibn Majah (4217)

Ad-dihhak ya kasance yana cewa: mun riski mutane sun kasance suna neman yadda ake yin tsantseni don haka suke yin tafiye-tafiye domin koyar yadda ta ke, yakan ɗauke su wata uku ko ma watanni masu yawa. Amma sai ga shi yanzu ba a damu da neman ilimin tsantsene ba, ballatana yin aiki da shi, ko da kuwa an fahimci muhimmancin sa.

Marigaya na ƙwarai sun kasance yayin da kuɗin (dinari) waninsu ya faɗi a wani wuri, sa'anan ya tuna daga baya ya koma ya gan shi ba zai ɗauka ba. Sai ya ce, wataƙila wanina ne ya yarda wannan, ni nawa kuwa wani ya tsinta.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Rashin damuwa da aibin waɗansu tare da shagaltuwa da aibin kanka na taimakawa wajen yin tsantseni a addini.

2- Daga cikin tsantseni a addini akwai barin shubuha.

3- Yawan bincike ga alamuranka domin gudun aukawa cikin haram na daga nasarar da ci gaban imani.

4- Neman ilmi a wajen masu tsantseni domin shiriya.

## BABI NA SHIDA

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN KAUNAR JUNANSU DA NUTSUWARSU DA KUMA TAKAITA ZANCENSU

Daga cikin halayyarsu yawaita ƙauna, nutsuwa da rashin hayaniya, da karamcin zance, hakan kuma yana nuni ne da cikar hankalinsu, da kuma yawan yin shawara da taimako a tsakanin mutanen zamanin sa.

Yana daga zantukan Amirul-Muminin, Ali ɗan Abi Talib Allah ya ƙara masa yarda cewa: Mutum kan kai ƙarshen tsayinsa daga shekara ashirin da biyu (22), kuma hankalin mutum na kaiwa matuƙa daga shekara ashirin da takwas (28) ne, daga nan kuma duk abin da zai zo masa zuwa ƙarshen rayuwarsa duk jarabawa ce.

Ƙatada Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: mutane sun kasu kashi uku ne: akwai rabin mutum, da wanda ba kowa ba, da cikakken mutum.

Shi cikakken mutum shi ne wanda yake da hankali kuma ra'ayoyinsa abin amfani ne, rabin mutum shi ne wanda yake yin shawara da ma'abotan hankali kuma yana aiki da ra'ayinsu, wanda ba kowa ba kuwa shi ne mutumin da ba shi da hankali kuma ba shi da basirar fitar da ra'ayi kansa kuma baya shawara da kowa.

Sufiyan ɗan Uyayya Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: Mafi haziƙin dabba shi ne wanda ba ya da wadatuwa daga barin bulala, kuma mafi hankaltar mace ita ce wadda ba ta da wadatuwa daga barin miji, sannan mafi hankaltar mazaje shi ne wanda baya da wadatuwa daga barin yin shawara da ma'abota hankali.

Wahab ɗan Munabbah Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: Duk wanda yake cewa shi mai hankali ne kuma ba a samu damuwarsa da lahira ba maƙaryaci ne.

Ka sani ya kai ɗan'uwana, ka bi magabatanka managarta sai ka huta. Dukkan godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin halittu.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Mafi kyaun mutane shi ne mai hankali kuma mai shawara da ma'abotan hankula.

2- Rashin hayaniya da karamci da kuma damuwa da lahira alamu ne na cikar hankali.

3- Mai hankali shi ya gane cewa rayuwar duniya dukkaninta jarabawa ce.

4- Yawan damuwa da lahira na nuna cikar hankalin mutum.

## BABI NA BAKWAI

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN ZANTUKAN HIKIMA

Daga cikin halayyarsu yawaita yin shiru, da kuma magana cikin hikima da sauƙi ga ɗalibi. Waɗansu daga cikin magabata sun kasance suna cewa: "hikima naɓuɓɓugowa ne daga ɗabi'u huɗu:

1. Yin nadama daga aikata zunubi.
2. Tattali da tanadin mutuwa.
3. Ya shewar ciki.
4. Yin abokan taka da masu gudun duniya.

Yana daga cikin tarin zantukansu na hikima shi ne faɗin waɗansunsu da cewa: *"Na hore ka da hikima domin tana mai da mazaunayyan talakawa matsayin mazaunayyan masu mulki.*''

Yana daga cikin faɗin Imam Shafi'i cewa: "mafi karamcin mutane a duniya sune waɗanda suka huta daga yin hassada da ƙulle-ƙulle ga waɗansu mutane.

Yana daga ciki faɗin Mu'awiya Al-Aswad cewa: *"duk wanda yake neman alkairi mai yawa a wurin Allah, ka da ya yawai ta baccin dare da na rana.*

Kuma ya ce: *"Duk wanda ya nemi wata falala daga ƙasƙantattun mutane, ka da ya zargi kowa yayin da ya wulaƙanta.''*

Imamu Shafi'i ya ce:

*"Duk wanda ya kawo maka gulmar wani, zai kai taka gulmar. Duk wanda ya ɗauko zancen waɗansu gareka zai ɗauki naka zancen zuwa ga waɗansu, duk wanda ka faranta masa ya faɗi wani abu a kanka abin da baka kasance ba, hakanan kuma da za ka fusatar da shi zai faɗi abin da baya tare da kai.''*

Abu Umamah Allah ya ƙara masa yarda ya ce: *"Duk wanda rayuwarsa ba ta samar maka da amfani ba, ka da kayi kuka domin mutuwarsa.''* Kuma ya ce*: "Furuci da laifi na rusa mummunan ayyuka, maɗaukaka ba su gushe ba suna jarrabtuwa daga danginsu.*''

Ɗan Mas'ud Allah ya ƙara masa yarda ya ce: *"Kasƙantar da kai yana ɗaukakar da maƙasƙanci, girman kai na ƙasƙantar da maɗaukaki, duk wanda ya nemi shugabanci sai ya wahalar da shi, kuma duk wanda ya guje wa shugabanci sai ta bi shi.''*

Fudail ɗan Iyyad Allah ya ƙara masa yarda ya ce: *"Dukkan wanda aibinsa suka yawaita abokanansa za su ƙaranta.*

Yahya ɗan Mu'az Allah ya ƙara masa yarda ya ce:

*"Duk wanda ya zama mai haƙuri zai zama jagorar abokanansa, duk wanda ya zartar da fishinsa zai nutsa cikin kogin wulaƙantar shi. Ka sani ya kai ɗan'uwana, ka tsarkake zuciyarka daga soyayyar duniya da sha'awarta, ka kuma yawaita ambaton Allah. Yayin da ka tsarkake zuciyar ka a lokacin nan Allah zai baka iya furuci da hikima kuma ka kasance mai hikimar zamaninka.''*

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Sauƙaƙawa wajen karantarwa na nuni da irin hikimar malami.

2- Magulmaci maha'inci ne ga kowa.

3- Rashin girman kai na ɗaukaka mutum.

4- Tsarkakar zuciya na daga cikin hanyoyin samun hikima.

5- Haƙuri da rashin fishi na kawar da wulaƙanci sannan yana jagoranci.

## BABI NA TAKWAS

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN YAWAN AZUMI

Daga cikin halayyarsu yawaita yin azumi, da ƙarancin zance, hakanan yake halin malamai masu aiki suke.

Muhmmad Ar-rahbi ya kasance yana cewa: Duk wanda ya shigar da abinci ciki fiye da buƙatarsa, zai fita daga harshensa yawan surutu.

Ibrahimun Nakha'i Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: Duk wanda yake tunani zai zama mafi ɗaukakar mutanen kowanne majalisi, kuma mafi kwarjininsu, kuma mafi yawan kawaicinsu. Domin yin shiru kwalliya ce ga malamai kuma rufin asiri ne ga jahili.

Ma'aruf Al-kaukhi ya kasance ana cewa: zancen mutum cikin abin da babu ruwansa yana daga cikin dalilan da Allah ke tabbatar da shi.

Abubakar As-Siddiƙ Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yakan sa tsakuwa a cikin bakinsa, ya kasance a haka shekara da shekaru, har ya saba da rashin yawan zance. Don haka baya cire tsakuwa daga baki sai don cin abinci ko Sallah. Dukkan wannan ɗabi'ar ya kasance yana yin hakanne domin gudun yin zance a cikin abin da ba ruwan sa, sannan lokaci da mutuwa ta zo masa ya kasance yana riƙe da harshensa yana cewa: *"wannan shi ne abin da ya kai ni inda ya kai ni."*
Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Yana daga cikin kyaun musulunci mutum barin abin da babu ruwansa"*[79]

[79]Tirmidhi (9/196) da Ibn Majah (3976)

An karɓo daga Shufaiyi ɗan Mati'i Al-Asba'i ya ce: ''*Wanda duk ya yawaita surutu kurakuran shi za su yawaita".*

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Yawan azumi da kawaici yana sanya basira.

2- Yawan surutu aibi ne ga mutum.

3- Harshe shi ne jagora wajen hallakar da mutum ko tseratar da shi.

4- Sanadiyar taɓewar mutum shiga al'amarin da ba bu ruwansa.

## BABI NA TARA:

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN RUFE DUK WATA KOFA TA GULMA A WAJEN ZAMANSU

Daga cikin halayyarsu sun kasance suna rufe ƙofar yin (gulma) da wani a wurin zamansu, domin ka da wurin zamansu ya koma wajen yin laifi. Don kyawawan ayyukansu baya iya tinkarar yi da wani (giba) sau ɗaya a ranan Kiyamah.

Waɗansu sun kasance suna yawaita ayyuka nagari domin kowane ɗaya daga cikinsu ya koma lahira da wani abu na aikin alheri domin ya ba da haƙƙoƙin dukiya ko mutuncin waɗanda za su yi jayayya da shi.

Allah (Maɗaukacin sarki) ya ce: *"Kada ɗayanku ya yi gibar (yi dawa ni) ɗayanku, shin ɗayanku zai so ya ci naman ɗan'uwansa matacce? Don haka sai ku ƙyamaci hakan (yi da wani)"*[80]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

*"Kun san mece ce giba? Sai sahabai suka ce Allah da manzonsa ne suka fi kowa sani, sai ya ce: "giba ita ce ambaton ɗan'uwanka da abin da baya so. "Sai suka ce, ya Manzon Allah, idan abin da aka faɗa yana tare da shi fa? Sai ya ce: "in abin da aka faɗa haka yake shi ake kira da giba. Amma idan abin da aka faɗa ba haka yake ba wannan shi ne ƙagaggiyar ƙarya (Buhtaanan)"*[81]

Sufyanut Thauri Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: "*Ka ambaci ɗan uwanka yayin da baka tare da shi, da kwatankwacin abin da ka ke so ya ambace da shi yayin da shi ma baya tare da kai.*''

---

[80](Hujurat 12)

[81]Abu Dawud Wassila Muslim (16/142) Al-Birru Wassila Ad-Darimi (2/299)

Malik ɗan Dinar Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ''*Ya isa mutum zama mai laifi kasancewarsa ba nagari ba (Salihi), sannan kuma ya zauna a wuraren zama yana cin mutuncin mutanen kirki (Salihai).*''

Muhammad ɗan Sirin Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa:

*''Yana daga cikin irin giba da aka haramta wanda mafi ya yawan mutane ba su ankara da ita ba, zancensu da cewa wane yafi wane ilmi, domin wanda aka ce an fishi zai sami damuwa, don haka abin kiyayewa shi ne, giba, ita ce ambaton ɗan'uwanka da abin da baya so.''*

Ya kai ɗan'uwana sai ka kawar da kai daga irin waɗannan al'amura, ka duba ka ga shin kai ka kuɓuta daga aukawa a ciki, sai ka godewa Allah maɗaukaki, ko ko kana ciki? sai ka nemi gafarar Allah.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Yin giba zunubi ne mai girma.

2- Duk abin da za a faɗi ko a aikata da ya zama cuta ga wani haram ne.

3- Hana yin giba a wurin zaman mutane ɗabi'ar muminai ne.

4- Dukkan zance da zata ɓatama mutum rai idan ya ji ba shi da kyau.

## BABI NA GOMA:

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN NISANTAR WASUWASI A WAJEN ALWALA DA IBADUNSU

Daga cikin halayyarsu rashin yin kokonto ga Alwala, da Sallah da sauran ayyukan ibadu. Tare da cewa kowane ɗayansu na ƙoƙarin tsantseni wajen ganin ya kai matuƙa a yayin ibadah. Domin kokonto daga shaiɗan ne kuma daga zaluncin zuciya ce.
Ita kuwa zaluncin zuciya tana daga cikin zaluncin ayyuka. Zaluncin ayyuka na daga cin haramun da shubha. Don haka duk wanda yayi taka tsantsan wajen cin halal shaiɗan ba zai sami kowane irin iko akan sa ba.

Waɗansu mutane sun ci daga abincin zalunci da kuma kwace, sannan suka zama suna neman kasancewa tare da Allah, da kuma samun tsoron Allah (khushu'i) a cikin ibadunsu amma haka bai samu ba.

Sai dai abin da ya kai ga matuƙar samun ɗayansu shi ne damuwa, da gajiyawa da kuma ruɗani na son zuciya a cikin halin yin niyyar yin Sallah, kamar yana farautar wani abu da ya kuɓuce a hannunsa. Don haka lokacin da ya yi kabbarar fara Sallah zaka ga yana cewa: AK, AK ,AK, BAR, BAR, BAR.

Haƙiƙa waɗansu daga cikin malamai sun yi fatawar ɓacin irin wannan Sallar da cewa: wannan ba zikiri ba ne. Domin idan ka ce wa ɗayansu ka yi alwala kamar yadda ya zo maka daga Manzon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi sau da yawa ba ya yarda kuma ba ya ƙudurce ingancin hakkan ba.

Muna roƙon Allah rangwame daga wanann irin ɓata bayyananne, da kuma mummunan ƙagaggen al'amari. Domin haka na daga kokonton shaiɗan, kuma lallai

haka baya da ga cikin tsarin Musulunci ko Imani. Dukkan yabo sun tabbata ga Allah Ubangijin talikai.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Haram ne hana natsuwa a ibada kuma ya sanya ruɗani a ciki.

2- Tsayuwa kan halal na rinjayarwa daga sharrin shaiɗan.

3- Kyale karantarwar Annabi yana la'anta ibada da samar da hasarar lahira.

## FASALI NA BIYAR

### BABI NA DAYA

### ƊABI'UN MAGABATA WAJEN ƁOYE SIRRIN 'YANUWANSU.

Daga cikin halayyarsu ɓoye sirri da rashin gayawa wani abin da ya zama haƙƙin jinsu su kaɗai. Haƙiƙa sun kasance suna cewa: 'yantacciyar zuciya kamar ƙabari ne mai rufin asiri. Ma'anar annamimanci shi ne ɗaukar zance da niyar ɓata tsakani, daidai ne ya cutar da wanda aka cirato zancen daga gare shi ko wanda aka kai masa ko wanda ya saurara. Wasu kuma suka ce annamimanci shi ne abin da duk in an bayyanar da shi bayyanarwar zai kawo ƙyama da rashin jin daɗi.

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Ba zai shiga aljanna ba mai annamimanci"*[82]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya faɗi wannan hadisin ne a ƙarƙashin faɗin Allah Maɗaukakin sarki: *"Matarsa (Abu Lahab) ma'abociyar ɗaukar ƙirare"*[83]. Ya ce "Matar (*Matarsa Abu Lahab)* ta kasance annamimiya ce (mai ɗaukar zantuttuka na ɓatanci daga nan zuwa can)''.

Yahya ɗan Abi Kathir Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa:

*Annamimi ya fi zamewa mafi sharri daga mai sihiri amma babu wanda ya fahimce shi. Domin annamimi a ɗan ƙaramin lokaci (sa'a ɗaya) yana aikata abin da mai sihiri bai aikatawa a wata ɗaya. Annamimi mai kaiwa ne ga zubar da jini, halaka dukiyoyi, kunna babbar fitina, raba mutane da garuruwansu da waɗansu ɓarna daban-daban masu yawa.''*

[82]Bukhari (10/472), Muslim (2/113), Tirmidhi (8/182) da Abu Dawud (13/219)
[83](Al-Masad aya 4)

Khalid ɗan Sufiyan Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ''*ku yi wa annamimi azaba (horo mai tsanani) ko da ya zame mai gaskiya ne, domin annamimanci kamar riwaya ce karɓarta kuwa halarce, don haka sai ya zamo karɓarta ya fi sharri akan ɗaukota.''* Ka sani ya kai ɗan'uwana, ka kiyayi yaɗa sirrin 'yan uwanka, ko ɗaukar zancensu zuwa ga waɗansu. Godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin halitta

WANNA BABI YANA KOYARDA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Haramcin annamimanci ko da ba zai cutar ba.

2- Sharrin annamimanci ya fi na mai sihiri da boka.

3- Wajibi ne ɓoye sirrin ɗan'uwanka.

## BABI NA BIYU:

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN SHAGALTUWA DA LAIFUKANSU AKAN NA WASU.

Daga cikin halayyarsu shagaltuwarsu da laifukan kawunansu daga barin laifukan mutane da kuma ƙoƙari wajen ɓoye laifufukan waɗansu. Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Shin in baku labari da mafi sharrinku, su ne masu yaɗawa da annamimanci, masu rarrabewa a tsakanin masoya, masu zaluncin da aibatar da mutanen kirki"*[84].

Waɗansu daga cikinsu kan ce: *Waninku kan ga aibin kansa amma tare da haka sai ya so ta, ya kuma nuna ƙiyayya ga ɗan'uwansa musulmi a bisa zato, ina hankali gayin haka?*

Yahya ɗan Maryam Allah ya ƙara masa yarda ya ruwaito cewa Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

*"Ka da ku yi dubi zuwa ga aibin mutane kamar cewa ku Ubangiji ne, sai dai ku yi dubi ne zuwa ga aibunku a matsayin bayi, domin mutane sun kasu kashi biyu ne: da wanda aka jarrabta da wanda aka yi masa rangwame, ku ji tausayin wanda aka jarrabta"*

Kuma Amirul muminuna, Umar ɗan Kaɗɗab Allah ya ƙara masa yarda, ya kasance yana cewa: *''Allah ya jikan wanda ya shiryar dani zuwa ga laifukana.''*

Ash-Sha'abi Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: '' *Wanda duk yake neman sanin aibin ɗan'uwansa zai ko zauna ba shi da aboki"*

Don haka ya kai ɗan'uwa ka kiyaye harshenka, domin duk wanda yake ta aljihun mutane za su keta aljihun sa.

Ahir ɗinka! da ka mantawa da kanka ya yin da kaga aibin ɗan'uwanka musulmi. A'a ya zama wajibi a kanka da kasanya aibin mutane ya zama tunatar da kanka ne aibobin

---

[84]Ahamd (6/459),(4/227)

ka. Domin duk asalinku guda ne, don haka duk abin da ya gudana ga waninka mai iya gudana ne gareka.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWAN KAMAR HAKA

1- Shagaltuwar mutum ga aibinsa tare da barin ambaton aibin waɗansu na nuna cikan hankali.

2- Jin tausayin wanda ke cikin jarabawar aikata aibi ɗabi'a ce ta muminai.

3- Nuna soyayya ga wanda ya shiryarda kai aibinka na nuna cikar hankali.

## BABI NA UKU

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN TAIMAKON 'YANUWANSU WAJEN AIKIN ALLAH.

Daga cikin halayyarsu yawaita kyauta da karamci da kuma miƙa dukiyoyinsu domin taimako da yalwatawa ga 'yan'uwansu a lokacin tafiye-tafiye da kuma lokacin halin zaman a gari. Domin da haka suke ƙarfafa junansu wajen taimakon addini, wanda shi ne manufarsu.

Abdullahi ɗan Umar Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana sanya sharaɗi ga duk wanda ke nufin ya abokance shi a lokacin tafiya da ya kasance bawan Allah ne domin ga irin shi zai yi taimako.

An tambaye Abdullah ɗan Mas'ud Allah ya ƙara masa yarda da cewa: Wane ne mai hankali? Sai ya ce wanda yake ɓoye dukiyarsa a inda tsutsa ba zata ci ba kuma ɓarayi ba za su sace ba, ma'ana a sama kenan.

An kira Abdullahi ɗan Jafar Allah ya ƙara masa yarda wajen walima sai bai jeba saboda waɗansu dalilai da suka hana shi, amma sai ya aikawa mai yin walimar da Dinari ɗari biyar (500), kuma ya gaya masa uzurinsa, ya kuma neme shi da ya yi masa rangwame a rashin halartarsa.

Sa'ad ɗan Ubada Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: Allah ka azirtani da dukiya da zan yi kyauta da ita, domin aikin kirki baya yuwuwa sai da dukiya, sannan sai ya rera wannan waƙar kamar haka:

*Ina ganin zuciyata tana son aikin alkhairi,*
*sai ta taƙaita ba tare da dukiyata ta kai ga matuƙa,*
*zuciyata taƙi kwaɗaitar min da rowa,*
*kuma tare da cewa dukiyata ba zata kai ni ga ayyukan alheri na ba.*

Ka sani ya kai ɗan'uwana, kuma ka kiyayi baiyanar da nagarta alhalin kana kan saɓanin mutane masu halin karamci, da kyauta, da taimako. Sun kasance suna ba da dukiyarsu mai yawa, ba su ganin samun yalwantarsu akan wani.

Dayansu ya kasance yana iya raba mayafinsa gida biyu ya yi kyauta da rabi ga wani. Haƙiƙa sun kasance idan mai roƙo ya zoma su, sai su ce: madalla da wanda ya zo domin ya ɗauki guzurinmu zuwa lahira ba tare da kuɗin biya ba, kuma ya sauƙaƙa mana daga abin da ya shagaltar da mu daga barin bautar Ubangijinmu.

Sun kasance idan mai hidimar dayansu ya rasu sai su aika masa wani mai hidimar. Kuma sai ya karɓa ba tare da ya ce wani abu ba, kuma basa ganin wani fifikonsu akan ɗan'uwansa.

Kuma sun kasance idan labari ya cin musu akan bashin waninsu, Sai su biya masa ba tare da sun shawarce shi ba. Don haka wanda ake bi bashi ya yin da ya fahimci haka sai ya yi shiru kamar ya riga ya biya daga dukiyarsa, domin saninsa da cewa hakan na daɗaɗa zuciyar ɗan'uwansa.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Manufan kyauta domin musulmi su ƙarfafa juna domin ciyar da musulunci gaba.

2- Yin abokantaka da mu'amala ya zama da mai tsoron Allah.

3- Halarcin neman dukiya domin yin ayyukan alheri.

4- Begen samun dukiya domin yin alheri na da kyau.

5- Kawar da rowa da jin daɗi yayin kyauta ko sadaka ga wani.

6- Fitar da musulmi daga damuwa ko ƙunci ɗabi'a ce abir ƙauna.

BABI NA HUDU

HALAYYAR MAGABATA WAJEN SAKIN FUSKA DA FARANTAWA JUNA RAI.

Daga cikin halayyarsu tsananta soyayyarsu a wajen aikata abubuwan da suka dace ga ‘yan’uwansu, da kuma son shinfiɗa fuska gare su, tare da son sanya farin ciki ga junansu. Kuma da fifita ‘yan’uwansu akan kansu wajen alheri.

Sun kasance ba sa jinkirin wajen tabbatar da haƙƙoƙin ‘yan’uwansu. Su kan ce: idan ɗan’uwanmu bai kasance wanda ya cancanci samun alheri kaza ba to mu muna cikin danginsa.

Muhammad ɗan Hanafiya Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *‘‘Duk mai aikata alkairi baya faɗuwa ko ya faɗi ba ya karyewa.’’*

Fudail ɗan Iyyad Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *‘‘Mu mun kasance ba ma ƙidanya bashi daga cikin abubuwan alheri, domin wanda ya bayar yana jiran a biya shi, don alheri na daga cikin yin sauƙi da yafiya ga mutane a cikin dukkan abin da suke nema a gareka duniya da lahira.’’*

Waɗansu sun kasance suna cewa: ‘‘*Ayyukan alhairai sun ƙare abin da ya rage kawai sai kasuwanci, don haka wani sai ya ba ɗan’uwansa wani abu da niyyar ya bashi.*’’

Abdullahi ɗan Abbas Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ‘‘Ayyukan alkhairi ba sa cika sai da abubuwa uku: gaggauta shi, da ganin ƙarancinsa ga idanuwan mai badawa, da kuma ɓoye shi daga mutane ya yin badawa.’’

Jafarn Muhammad Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: Tir da mutumin da baya iya gaba-gadi buɗewa ɗan’uwansa jakarsa a lokacin da baya nan domin ɗan’uwan ya ɗauki abin da yake so ba tare da izninsa ba.

Haƙiƙa ɗayansu kan iya aika ta hakan saboda abin da ya sani na halin rowan ɗan’uwansa, tare da ƙaddarta hakan ga kansa.

Ibrahim ɗan Adham ya kasance yana cewa: *''Mun riski mutane wanda ɗayansu baya ganin shi ke da haƙƙin a kansa fiye da ɗan'uwansa, sai dai inya kasance ya fi buƙatuwa gare shi daga ɗan'uwansa.''*

Wani mutum ya ce da Aws ɗan Kharijah Allah ya ƙara masa yarda ya ce ni na zo maka cikin wata ƙaramar buƙata. Sai ya ce masa, ka je ka neman mata ƙaramin mutum.

Ya kai ɗan'uwa! Don haka sai ka bincike kanka, shin kana kan tafarkin tsarin rayuwar managarta magabata a cikin irin abin da ka karanta ko ka saɓama musu. Kashedinka! Da zaton cewa kana cikin bayin Allah managarta alhalin baka cikinsu.

WANNAN BABI YANA KOYARDA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Ana son gaggauta aikin alheri da ganin ƙarancin lokacin bayarwa, kuma ɓoye shi daga barin idanuwan waɗansu mutane.

2- Ba a taɓewa yayin da aka yi aikin alheri .

3- Fifita 'yan'uwa a cikin arziƙi da yawaita alheri gare su.

4- Koƙarin yin aikin zama mutumin kirki ba taƙaituwa da bege ba.

BABI NA BIYAR

HALAYYAR MAGABATA WAJEN KARRAMA BAKO DA YI MASA HIDIMA.

Daga cikin halayyarsu girmama bako, da yi musu hidima da kansu, sai dai idan da akwai wani uzurin shari'a. Kuma ba sa ganin cewa su sun ciyar da shi abincin da ya dace da shi, ko sun yi masa hidima da ta kamance shi a lokacin da yake tare da su, kuma tare da zaton sun kyautata masa.

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Wanda ya yi imana da Allah da rana ta ƙarshe sai ya girmama baƙonsa.'' suka ruwaito shi.*[85]

Ya zo a cikin Bukhari da Muslim daga hadisin Abi Shuraih Allah ya ƙara masa yarda ya ce:

*"Idanuwa na sun ga Manzon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi kunnuwana sun ji Manzon Allah Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya yin da aka yi magana da shi. Sai ya ce: Duk wanda ya yi imani da Allah da rana ta ƙarshe sai ya girmama haƙƙin baƙonsa. Sai suka ce: Mene ne haƙƙinsa? Sai ya ce yini da dare. Kuma ya ce baƙunta kwana uku ne duk yayin da ya wuce haka daganan (hidima gare shi) sadaka ne.'*[86]

Imam Muslim ya ruwaito hadisi daga Shuraih cewa daga Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

*"Baƙuntaka kwana uku ne, amma haƙƙin baƙon yini da dare ne. saboda haka duk abin da aka ciyar da shi bayan kwana uku sadaƙa ne. kuma baya halatta da ya (shi baƙon) zauna a gurinsa ( mai masaukinsa) har sai ya kai shi da yin aikin zunubi. Sai suka ce:*

---

[85]Bukhari (10/532), Muslim (2/18), Abu Dawuda (5132), Ibn Majah (3,971) da Tirmidhi (8/145)

[86]Bukhari (10/531), Muslim (12/31), Abu Dawud (3,730) da Tirmidhi (8/145)

*ya ya zai yi aikin zunubi? Shi ne baƙon ya tsayu a gurin ( mai masaukinsa) har ya kai lokacin da ba zai iya yi masa hidima ba'*[87]

An-Nawawi ya ce Malamai sun ce abin da ake nufi shi ne nuna damuwa da baƙo a yinin farko da darensa, ta hanyar jiyar da shi daɗi da zamewa tare da shi gwargwadon ƙa'idar shari'a. Amma a rana ta biyu da ta uku sai ya ciyar da shi da abin da ya sauƙaƙa gare shi kuma wanda bai wuce al'adun rayuwarsa ba. Amma bayan kwana uku komai ya yi masa sadaka ne abin sani in kuma yaso ya bari.

Anas ɗan Malik Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa "Zakkar gida'' shi ne samar da ɗakin baƙi a ciki.

Waɗansu sun ce game da zargin rowa da rashin tsayuwa da haƙƙoƙin baƙo. Idan kana so samun 'yan'uwantaka ta musulunci da soyayyar Allah, Sai ka ɗauke idanuwanka daga abincin baƙonka. Mutuwa ta fi sauƙi da a hana baƙo loma ɗaya. Ya kai matuƙar muni kan ragewar gurasar ko ragewar wani abu daga ƙashin taunawar da za ka bawa baƙonka. Ka kiyayi ruɗin shaiɗan kan kyautatawarka ga baƙonka.

WANNAN BABI YANA KOYARDA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Saukar da baƙo da hidima gare shi na daga cikin kyakkyawar ɗabi'a mai nuni da imani.

2- Bai halatta baƙo da mai masaukinsa su saɓawa shari'a ba ga bin ƙa'idar baƙunta.

3- Baƙuntaka kwana uku ne amma haƙƙin shi yini da dare ne kawai.

4- Daga cikin tarbiyan musulunci samar da masaukin baƙo a gida.

5- Yin rowa aibi ne mai tsanani.

---

[87]Muslim (12/13)

## BABI NA SHIDA

## ƊABI'UN MAGABATA WAJEN KIN AMSA GAYYATAR CIN ABINCIN DA YAKE NA HARAMUN NE.

Daga cikin halayyarsu rashin amsa gayyata zuwa ga cin abincin wanda abincinsa haramun ne, ko kuma yayin da ya kirayi mawadata banda talakawa zuwa ga cin abincin, ko kuma ya zama wuri da aka yi kiraya domin waliman akwai sabawa Allah. Kuma sun kasance suna kamewa daga abin dake hannun mutane na halal.

Abu Mas'ud Al- Baɗari Allah ya ƙara masa lafiya ya kasance baya amsa gaiyatan walima sai in ya tabbatar da babu wani abu na saɓon Allah a cikinta.

Abu Ayyub Al- Ansari Allah ya ƙara masa lafiya ya kasance idan ya tafi wurin walima sai ya ga gidan an lulluɓe shi daga katangar gidan sai ya koma, yana mai cewa ba mai lulluɓe gida sai mugaye kangararru, mu bama cin abinci a wurin irin waɗannan mutanen. Waɗansun daga magabata sun kasance suna cewa: babu sauran sunna a cikin walima. Da ya kasance manyan kwanuka cike da nama ake ciyarwa da ita a masallaci ga duk wanda ya zo, mai arziƙi ne ko talaka ne, babban mutum ne ko ƙasƙantacce sai ya ci.

Amma yayin da mai walimar ya keɓance gayata ga attajirai kawai, sauran mutumen ba za su ci abincin daga gareshi ba kenan, sai su ce wannan shi ne mafi sharrin abinci.

### WANNAN BABI YANA KOYARDA ABUBUWA KAMAR HAKA :

1- Baya halarta a kawo kowane irin aiki ko zance a wurin yin walima.

2- Baya halartar amsa gayyatar walima da za a saɓama Allah mai tsarki da ɗaukaka.

3- Mafi kyaun walima a gayyaci kowa da kowa.

## BABI NA BAKWAI

## ƊABI'UN MAGABATA WAJEN YAWAITA SADAKA DA RANA DA KUMA DARE A BAYYANE DA KUMA ƁOYE

Daga cikin halayyarsu yawaita yin sadaka cikin dare da rana a ɓoye ko a bayyane da ga dukkan abin da ya wuce buƙatuwarsu. Kuma duk wanda misali bai sami kuɗi ko abinci ba sai ya yi sadaka da kamewa daga barin cutar da mutane tare da ɗaukar nasu cutarwar.

Allah Maɗaukakin sarki ya ce: *"Waɗanda ke ciyar da dukiyoyin su cikin dare da yini, kuma a ɓoye da bayyane suna da ladan su wajen Ubangijinsu ba su da tsoro ko damuwa a kansu"*[88]

Allah Maɗaukakin sarki kuma ya ce: *"Ba za ku taɓa zama masu ɗa'a ba har sai kun ciyar daga mafi soyuwa a wurin ku"*[89]

Abdul'aziz ɗan Umair Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ''*Sallah na kai ka zuwa rabin nisan hanya, kuma azumi na isar da kai kofar mulki, sannan sadaka tana shigar da kai wajen Mai mulki (Allah).''*

Ya kuma kasance yana cewa: ''*Dukiya a wurin mu kayan ajiya ne na karamci. Ya kasance daga halayensu (magabata) yawan sakin fuska ga wanda yake roƙo, da kuma kyautata zato gareshi da cewa bai roƙa ba sai don buƙata.*''

Sufiyanut Thauri Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana farin ciki in ya ga mai roƙo a ƙofar gidansa, sai ya ce maraba da wanda ya zo ya tsabtace ni daga zunubina.

Fudail ɗan Iyyad Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ''*Madalla da masu roƙo suna ɗaukar mana guzurinmu zuwa lahira ba tare mun biyasu ba har sai sun kai sun ɗaura a kan ma'aunayyan da ke gaban Allah.*''

---

[88](Bakara aya 274)
[89](Ali-Imran aya 92)

WANNAN BABI YANA KOYARDA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Sadaƙa ba ta da wani keɓantaccen lokaci kodayaushe ana yinta.

2- Yin sadaƙa na ɗaukaka darajar mutum a wurin Allah.

3- Sadaƙa tafi soyuwa daga mafificin dukiyar mutum.

4- Barin cutar da mutane da ɗaukan cutarwarsu sadaka ne .

HALAYYAR MAGABATA WAJEN RIKO DA ABOKIN DA ZA SU GIRMAMA SHI

Daga cikin halayyarsu ba su ɗaukar wani daga 'yan'uwa face wanda suka san daga zuciyarsu cewa za su cika masa haƙƙinsa. Domin idan baka cika haƙƙin ɗan'uwanka ba zai zama wanda baya ganin ƙimarka a zuci. Amirul Mumunin Ali ɗan Abi Talib Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *''kashedinku game da 'yan'uwa! domin su tattalin duniya ne da lahira, shin ba ku ji zancen 'yan wuta ba 'Ba mu da mai cetonmu, kuma babu aboki majiɓinci' (Ash-Shu'ara:100 -101).''*

Imamus Shafi'i Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ''*ba don hirar 'yan'uwa ba a cikin wannan gidan, da kuma ibadar lokacin jijjifi da ban so zama a cikinsa ba.''*

Waɗansu (magabata) sun ce:

*''Yana kamata ga mai hankali da ya nisance 'yan'uwantaka da mutum uku: wawa da maƙaryaci da kangararre (fajiri). Domin shi 'wawa' bai yi maka nuni da alheri, kuma ba a zaton shi da kawar da sharri, kuma shirunsa ya fi alheri daga maganarsa, kuma nisantarsa ya fi kusancinsa. Shi kuwa maƙaryaci tarayya da shi ba ya taimakawa ga rayuwarka, domin zai ɗauki zancenka ne zuwa ga waninka, kuma zai ciyar da ƙiyayya da gaba tsakanin ka da mutane. Amma kuma kangararre (fajiri) zai ƙoƙarin ƙawata maka aikinsa ne, ba kuma zai taimake ka ba da wani al'amarin kan addininka. Ka sani ya kai ɗan'uwa ka kuma binciki kanka, ka duba shin ko ka cika da haƙƙoƙin 'yan'uwanka, shin ko ka kame daga roƙonsu ta nuna hali ko zance ko ta hanyar bijirowa da kai? Shin ka ko abokance su saboda Allah ko kuma domin wata manufarka ne?*

Domin duk abin da ba don Allah ba ne to sai ya zama damuwa ga bawa a duniya da lahira. Don haka ka nemarwa kanka ya kai ɗan'uwa haƙoƙin 'yan'uwa. Ka da ka nema daga garesu a bayyane ko a ɓoye haƙƙinka.

Imam Shafi'i ya rera waƙa:

*"Abokin da bai amfanarwa lokacin tsanani,*
*Ya kusanta ga abokin gaba ga ma'auni,*
*Ba a zalunta aboki da dukkan hani,*
*Kuma baya kamata ga 'yan'uwa sai haƙuri, mutane sun yawaita manema rawani na,*
*Ɗan'uwa amintacce fitununa sun wahalar da shi garuruwa sun ƙyamata a kaina har,*
*Ka ce kamar ba mutane ne ke cikinta ba"*

WANNAN BABI YANA KOYARDA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- 'Yan'uwantaka da ɗaukar hidimarsa na daga cikin koyarwar addini.

2- Ba a 'ya'uwantaka da wawa ko maƙaryaci ko kangararre (fajiri).

3- 'Yan'uwantaka ana yinta ne domin Allah kawai.

4- Cutar da 'yan'uwantaka haɗari ne a rayuwar musulmi.

## BABI NA TARA:

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN RASHIN RIGIMA DA KUMA MAYAR DA MAKIYI ZUWA MASOYI.

Daga cikin halayyarsu barin yin gaba da mutane, da kuma samar da haƙuri da yarda ga mutane ga dukkan hasara, tare da rashin fuskantarsu da mummunan abu, mutane na gaba da su amma su basa gaba da wani.

An ruwaito daga Annabi Dawud cewa shi ya cewa ɗansa: ya ɗana kada ka raina maƙiyi ko da ɗaya ne, kuma kada ka nemi yawaita kasancewar masoya dubu gareka.

Imamus Shafi'i ya rera waƙa yana cewa: *Masoya dubu ba su yi yawa ba ga mutum ɗaya…domin maƙiyi ɗaya ya yawaita.*

An ruwaito daga Ayuba Allah ya ƙara masa yarda da aka ce masa: Wane abu ne yafi cutar da kai lokacin da kake cikin jarrabawa? Sai ya ce: Dariyar maƙiya.

Don haka waɗansu daga magabata suka rera waƙa suna cewa:

*Dukkan abubuwan amfanin duniya ruɗi ne,*

*Duk mai farin ciki baya tabbata ga farin ciki,*

*Ka gaya wa masu farin ciki da damuwar mu su yi tanadi,*

*Domin fitinan duniya mai jujjuyawa ce.*

Muhammadu ɗan Muƙatil Allah ya ƙara masa yarda yana cewa: *Ka kiyayi sharrin wanda ka kyautata gare shi, ka yi wa ɗan'uwanka uzuri, da abin da ka yi wa kanka uzuri da shi.* Sai kuma ya ci gaba da cewa: *Ka nema kanka uzuri lokacin da ka munana… amma ga waninka ba ka bashi uzuri. Kana ganin ƙazanta a cikin idanuwansa… alhalin a cikin idanuwanka ga munin da baka gani.*

### WANNAN BABI YANA KOYARDA ABUBUWA KAMARA HAKA

1- Koƙarin rashin gaba da kore maƙiyi na da muhimmanci.

2- Gudun duk abin da zai ba maƙiyi dama ko dariya a kanka.

3- Koƙarin yin uzuri na alheri ga mutane na cikin tarbiyar musulunci.

4- Kada ka ɓata lokacinka wajen yin gaba da wanda ke gaba da kai.

5- Gudun duniya da lura da abubuwan ruɗi a cikinta na daga tsarin imani.

Daga cikin halayyarsu yawaita nisantar da kawunansu daga mutane maɓarnata Allah Maɗaukakin sarki ya ba da labarin Annabinsa Ibrahim Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yayin da ya cewa mutanen su:

*"Na ƙaurace muku da abin da ku ke bautawa koma bayan Allah, ina mai bautar Ubangijina da fatan ba zan zame mai taɓewa daga bautar Ubangijina. Yayin da ya ƙaurace musu da abin da suke bautawa koma bayan Allah sai muka yi masa kyautar Ishaƙ da Yaƙub kuma dukkaninsu mun sanya su Annabawa."*[90]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi Ya ce: *"Wani zamani zai zo ga mutane wanda fiyayyun dukiya ga mutum musulmi su ne dabbobi, da zai yi kiwonsu cikin dutwasu da matattarar ruwa, domin ya tsira da addinin shi daga fitina".*[91]

Hassan ɗan Salih Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *Haƙiƙa mun riski mutane waɗanda suna soyayya daga nesa-nesa, suna masu ƙyaman haɗuwa.*

Rabi'i ɗan Khaisan Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ''*Ba ya kamata ga wani ya ƙaurace domin yin ibada sai bayan ya fahimce addini.''*

Imam Malik Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *''ka yi ilmi sannan ka ƙaurace.''*

Sufiyanut Thauri Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *''Wannan zamanin shiru ne da kuma zaman gida, tare da wadatuwa da ɗan abinci har mutuwa ta zo maka.''* Kuma ya kasance yana cewa:

*''Mun riski waɗansu mutane su magani ne da ake neman waraka ta garesu, sai suka wayi gari yau ga cuta ba magani gareshi. Sai aka ce: nisantar kowa shi ne cikakken*

[90](Maryam 48,49)
[91]Bukhari (11/331)

*mutumci ka san haka ya kai ɗan'uwa ka yi mu'amala da mutane yayin da suka yi wa Allah biyayya, ka bar yin mu'amala da su a cikin saɓawa da biyan mafi yawan halal.* Godiya sun tabbatar ma Allah Ubangijin talikai.

WANNAN BABI YANA KOYARDA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Kyaun addinin mutum na danganta da nisantar shi daga maɓarnata.

2- Rashin yawan cuɗanya da mutane da ƙauracewa na da kyau ƙwarai ga mai ilmi.

3- Ya zama mafi kyaun imani yin hattara da abokantaka.

4- Yawaita shiru da rashin hayaniya na samar da kuɓuta da mutunci.

FASALI NA SHIDA

BABI NA DAYA

HALAYYAR MAGABATA WAJEN KARA KANƘANDAKAI A DUK LOKACIN DA SUKA SAMI WATA ƊAUKAKA.

Daga cikin halayyarsu akwai yawaitar da ƙasƙantar da kawunansu da neman kusanci da Allah a duk lokacin da waninsu darajarsa ta ƙaru. Daga cikin alamu ingattacce mai nuni ga walittakar mutum ga Allah shi ne duk lokacin da Allah ya ƙara masa girma shi kuma sai ya ƙara ƙasƙantar da kai da miƙa wuya zuwa ga bauta Allah.

Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Wancan gidan lahira mun sanyata ne ga waɗanda ba sa nufin ɗaukaka a ƙasa (duniya) ko kuma ɓarna, kyakkyawan ƙarshe na ga masu tsoron Allah"*.[92]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

*"Bazai shiga Aljannah ba wanda akwai kwatankwacin nauyin kwayar komayya (zarra) na girman kai a zuciyarsa. Sai wani mutum ya ce: mutum na son tufafinsa da takalmansa kyawawa. Sai Annabi ya ce: lallai Allah kyakkyawa ne kuma yana son kyau. Girman kai shi ne kawar da kai daga gaskiya da kuma wulaƙanta mutane"*[93]

Abu Muhsin Khaulani Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *Ba mai yin girman kai sai wulaƙantacce, ba mai alfahari sai ƙasƙantacce, ba mai goyon baya a kan ɓarna sai mai ƙasƙantaccen asali".*

Abu Hurairah Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana shugabancin Madina a zamanin Halifa Marwan ya ɗauki ɗaurin ice (ƙirare) a kansa daga kasuwa yana tafiya yana cewa ku buɗa hanya ga shugabanku.

---

[92](Al-Kasas aya 83).

[93]Muslim (2/89)

Abu Ayuba As-Sakhtiyan Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: *''Ya kamaci malami ya ɗora turbaya a kansa don ƙasƙantar da kansa ga Allah''.*

An karɓo daga Hassan cewa lokacin da ya tuna da wannan ayar: *"Waɗanda ke tafiya a bayan ƙasa suna masu natsuwa."*[94] sai ya ce:

*''Muminai su ne waɗanda wallahi jinsu da ganinsu da gaɓoɓinsu sun yi rauni har jahili kan yi zaton ba su da lafiya, ina kuma rantse ma da Allah ba wani rashin lafiya ke tare da su ba, wallahi lafiyarsu ƙalau, sai dai abin da ya shige su tsoron Allah ne wanda waɗansunsu ba su samu ba. Kuma babu abin da ya hana su jin daɗin duniya sai ilminsu game da lahira.''*

Sai suka ce godiya ta tabbata ga Allah wanda ya tafiyar mana da damuwa. Wallahi ba abin da ya sa su baƙin ciki ba daidai yake da abin da ya sauran mutane bakin ciki ba.

Kuma ba sa ganin girman duk abin da suke neman Aljanna da shi. Tsoronsu ga wuta ya sanya su kuka, domin duk wanda bai nemi girma da girman Allah ba ransa zata yayyanke yana mai nadama a kan duniya. Kuma duk wanda bai ga ni'imar Allah a gareshi ba, sai ga abinci, da abin sha, haƙiƙa ilminsa ya ƙaranta, kuma azabarsa ta riske shi.

Daga Anas ɗan Malik ya ce: *''Haƙiƙa na gani a tsakanin allon kafaɗar rigar Umar Allah ya ƙara masa yarda kecewa guda huɗu.''*

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA;-

1- Hanyar tsare ni'iman Allah shi ne rashin girman kai.
2- Kin karɓar gaskiya da wulaƙantar da mutane alama ce ta girman kai.
3- Aljanna ba ta karɓar masu girman kai a duniya.
4- Kwalliya da jin daɗin abubuwa ba shi ne girman kai ba.

---

94(Al-Furƙan aya 63)

## BABI NA BIYU

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN RASHIN BARIN DUK ABIN DA YAKE NA FALALA NE KO DA BA WAJIBI BA NE.

Daga cikin halayyarsu rashin wulaƙantar da wani abu na daga mustahabai da shari'a ta kwaɗaitar da aikatawa. Tare da cewa sun kasance suna ganin ba su da wata nafila a wajen aikata da'a, domin suna ganin yin nafila na ga wanda ya gama aikata wajibi ne.

Kamar yadda Allah maɗaukakin sarki ya ce ga Annabinsa: *"Daga cikin dare ka yi ƙoƙarin (ibadah ciki) ƙarin lada (nafila) ne gareka"*[95]

Sai ya sanya ta (ƙoƙarin Ibadun dare) ƙarin lada (nafila) ne ga haƙƙin Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi shi kaɗai saboda cikan farillansa.

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: ''Ka da ka wulaƙanta wani abu daga umarnin shari'a ko da kuwa haɗuwa ne da ɗan'uwanka da sakakkiyyar fuska.[96]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi kuma ya ce: *"Zance mai daɗi sadaƙa ne"*[97]

Hassanul Basari Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana yawaita ayyukan biyayya (ga Allah) kuma yana cewa: ba irinmu ba ne suke yin nafila, domin masu yin nafila su ne waɗanda ayyukansu na farilla suka cika.

Salmanul Faris Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ''*Misalin wanda yake yawaita ayyukan mustahabai kuma bai cika ayyukansa na farilla ba, kamar misalin ɗan kasuwa ne da ya yi hasarar uwar dukiyarsa kuma wai yana neman riba.''*

---

[95](Isra'i aya 79)
[96]Muslim (17/177) ya ruwaito shi.
[97]Ahmad (2/316) da Bukhari (6/85) suka ruwaito shi.

Yunus ɗan Ubaid Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ' *'Duk wanda ya ke sakaci da nafilfili zai yi sakaci da farillai.''*

Ka sani ya kai ɗan'uwana, yana kamatuwa ka yawaita nafilfili da ayyuka masu falala kada ka ƙosa daga garesu, ba ka ganin bayan haka idan ka tsayu da wajibabbu godiya ne ga ni'ima guda daga cikin ni'imomin Allah a gareka. Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Girmama kowane umarni na addini da rashin ganin muhimmancinsa.

2- Kyautata ayyuka wajibai kafin yin nafila.

3- Yawaita nafilfili bayan farilla.

4- Yawaita waiwaye da fahimtar ni'imomin Allah ga mutum domin gode masa.

## BABI NA UKU

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN YAWAITA NEMAN GAFARA DA DARE DA RANA

Daga cikin halayyarsu yawaita komawa ga Allah da neman gafara cikin dare da yini. Domin sun tabbatar wa kawunansu cewa ba su iya kuɓuta daga yin zunubi a cikin aikata ayyukansu na rayuwa da na ibadu. Don haka suke neman gafara domin gazawarsu wajen zuwa da abin da ya umurta na ƙa'idojin addini da tsoron Allah a ciki. Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Ku tuba zuwa ga Allah ya ku muminai ko kwa rabaunta."*[98]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Wallahi ni ina neman gafarar Allah kuma ina komawa gareshi a yini sama da sau saba'in"*[99]

Waɗansu daga cikin magabata sun ce: *Duk wanda bai neme tuba ba safiya da yammaci to ya kasance daga cikin azzalumai.''*

Allah maɗaukakin sarki ya ce: *"Duk wanda bai tuba ba to waɗannan su ne azzalumai"*[100]

Yahya ɗan Mu'az ya kasance yana cewa: *Zamewa (daga hukuncin addini) sau ɗaya bayan tuba tafi zamewa saba'in kafin tuba".*

An tambayi Sufiyan ɗan Uyayna alamun tuba ta gaskiya? Sai ya ce: Abubuwan huɗu ne: Ganin rashin ƙimar duniya da jin ƙasƙanci ga kanka da yawaita ayyukan da'a domin neman kusanci da Allah, da kuma ganin ƙaranci da gazawa ga ayyukan addini.

---

[98](Nur: aya 31).
[99]Bukhari (11/101) da Muslim
[100](Al-Hujirat aya 11).

Fudail ɗan Iyyad Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa masu tafiya jihadi lokacin fitarsu: *''Ku yawaita tuba domin tana muku kariya fiye da kariyar takubbanku.''*

Amirul Muminuna Umar ɗan Khaɗɗab Allah ya ƙara masa yadda ya kasance yana cewa: *''Ku zauna wajen masu yawaita tuba domin suna sa zukata su yi taushi.''*

Ka sani ya kai ɗan'uwa ka yawaita tuba (istigfari) matuƙar kana cikin gidan duniya. Don tuba na kawar da fishin Allah (Al- Jabbar). Kuma ka da ka zaci shafewar zunubanka domin ka aikata al'amuran da aka ce a shari'ah suna kankare zunubai, tana yiwuwa akwai wasu sharuɗan da baka aikata ba. Kuma ka sani shi Mumini baya da cikakkiyar natsuwa har sai ya ga kansa a cikin Aljanna. Ka fahimci hakan dukkan godiya sun tabbata ma ubangijin talikai.

WANNAN BABAI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Yawaita fahimtar gazawa da aikata zunubi domin tuba da istigfari.

2- Yawan tuba da istigfar garkuwa ce daga sharri kuma mabuɗin alheri ne ga mutum.

3- Yawaita tuba ko zama tare da masu tuba na sa taushin zuciya domin karɓar addini.

## BABI NA HUƊU

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN UMARNI DA KYAKKYAWAN AIKI DA KUMA HANI DA MUMMUNA

Daga cikin halayyarsu yin umarni da kyakkyawan ayyuka da kuma hani daga munanan ayyuka ko da kuwa ba su aikata ba ko ba su hanu ba. Haƙiƙa waɗansu sun yi tunani da cewa yin umarni da kyawawan ayyuka ko hani daga munanan ayyuka bai yiwuwa mutum ya gudanar da su sai ya zama tsarkakakke daga dukkan aibi ko ya tsarkaka daga dukkan ƙazantar saɓon Allah.

Lallai irin wannan zaton mumuna ne da za a ce kowane mutum ba zai yi umarni da kyakkyawan al'amari ba kuma ba zai yi hani daga munanan ayyuka ba har sai shi ya zartar da hakan ga kansa da ba bu wanda zai yi aikin umarni da kyakkyawa ko hani daga mummuna. Waɗansu daga magabata sun ce: ''Idan da za a ce mai zunubi ba zai yiwa masu laifuffuka wa'azi ba….. to waya isa ya yi wa masu laifuffuka wa'azi bayan Annabi Muhammad Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Allah Maɗaukakin sarki ya ce: *"Lallai a sami wata Jama'a daga cikinku, waɗanda za su kira zuwa ga alheri kuma su yi umarni da kyawawa da hani ga munana, waɗannan su ne masu babban rabo"*[101]

Allah Maɗaukakin sarki ya ce: *"Kun kasance mafi alherin al'umma da aka fitar da ku daga mutane kuna umarni da kyawawa kuma kuna hani daga munana sannan kuma kun yi imani da Allah"*[102]

Annabi Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: *"Duk wanda ya ga wani abu mummuna daga cikinku ya canja shi da hannunsa, idan ba zai iya ba ya canja shi*

[101](Ali-Imran aya 104)

[102](Ali-Imran aya 110).

*da harshensa, idan ba zai iya ba ya canja shi da zuciyarsa, hakan (amfani da zuciya) shi ne mafi raunin Imani''*[103]

Huzaifah ɗan Yamani ya kasance yana cewa: '*'Zamani zai zowa mutane zai kasance wajen firar mutane kamar mushen jaki ne, kuma mushen jakin zai fi soyuwa a wajensu fiye da wajen firar muminai, waɗanda ke umartarsu kyawawa kuma suke hana su munana.''*

An cewa Sufyanut Thauri Allah ya ƙara masa yarda shin mutum zai umarci wanda ya san ba zai karɓa ba? Sai ya ce: *''eh, don hakan ya zama masa uzuri a wajen Allah.''*

Malik ɗan Dinar Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ''kyawawa abubuwa sun tafi yana kuka, munana sun tunkaro yana dariya. Sannan sai ya rera waƙa:

*Mazajen da ake koyi da ayyukansu,*

*Masu musanta dukkan al'amura munana sun ƙare,*

*Na wanzu cikin 'yan baya waɗanda suke tsarkake junansu,*

*Ta yadda kowanne mai mummunar ɗabi'a ke tunkuɗe wa ɗan'uwansa.*

Ya kai ɗan'uwa sai ka kawar da kanka daga waɗannan siffofi kuma ka yi bincike akan shin kana a cikin waɗanda ake ƙyama ko a'a? Shin kana cikin waɗanda suke son Allah ko a'a? Shin ko ka taimaki shari'ar Annabinka ko ka kyale ta? Domin mafi yawan mutane a yau sun ƙyale tafarki (Shari'ah) tsarkakka ga zantukansu da ayyukan su da shirunsu a kan munanan abubuwa. Babu wata dabara babu wani ƙarfi sai ga Allah.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1. Yin umarni da aikin alheri ko hani daga mummuna ba sai wanda ya zama tsarkakke ne kawai zai yi ba.

---

[103]Muslimi (2/22,25), Tirmidhi (9/18,19), Abu Dawud (1128) da Ibn Majah (431)

2. Mafi kyaun musuluncin mutum shi ne hani ko ƙyaman munanan ayyuka.
3. Nisanta da ƙiyayyar wajajen hira da babu ambaton Allah da Annabi.
4. Ana yin wa'azi ga kowa har wanda ake zaton ba zai karɓa ba.

## BABI NA BIYAR

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN NISANTAR JIJI DA KAI.

Daga cikin halayyarsu rashin mamakin kai da lura da ayyukansu a matsayin dalili. A'a sai dai suna ganin rashin cika da giɓi a cikin ayyukansu na ɗa'a, ballantana kuwa ayyukansu munana.

Mudarrif ɗan Abdullah Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *''Da in kwana ina bacci in wayi gari cikin nadama ya fi soyuwa a gareni da in kwana ina tsayuwar dare in wayi gari ina mai jiji da kai".*

Hassanul Basari Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *''Da a ce dukkan ayyukan mutum kyawawa ne da mutum ya hallakar da kansa saboda taƙama. Amma sai dai Allah ya jarrabce shi da fahimtar gazawar shi domin rahama a gare shi".*

Magabata sun kasance ya yin da aka yabe wani da alheri a wurinsu sai su ce: *''Ya Ubangiji ka sanya ni mafi alkhairin abin da suke cewa ka kuma gafarta min daga abin da su ba su sani ba.''*

Umar Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *''Ya Ubangiji ina neman tsarinka daga sharrin abin da suke cewa kuma ina roƙonka da ka gafartamin abin da su ba su sani ba.''*

Bushrul Hafi Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *''Idan kaga mutum mai tsananin naci, mai alfahari da ilimi kuma mai jiji da kansa, ka sani cewa ya cancanci dukkan hasara.''*

Duk da cewa magabata sun kasance masu matuƙar yin ƙoƙari wajen ibadah da kuma barin yawan sha'awa tare da haka ba sa gamsuwa ga kansu. Irin wannan tafarki shi ne al'umma ta yarda akai, kuma duk wanda ya saɓa musu haƙiƙa ya keta abinda suka haɗu a kansa.

Abdul-Aziz ɗan Abi Rawwada Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: *''Idan ka kawo labarin magabata a tsakaninmu dukkanmu sai mu ji kunya.''*

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Rashin taƙama da yawan ibada.

2- Fahimtar da kai gazawa wajen yima Allah biyayya.

3- Rashin alfahari da ilmi da taƙama da samu domin gudun halaka.

4- Roƙon gafara da ganin yawaituwar zunubi.

## BABI NA SHIDA

## HALAYYAR MAGABATA WAJEN YADDA SUKE SHIRYA TSAYIWA A GABAN ALLAH.

Daga cikin halayyarsu yin kyakyawan shiri wajen tsayuwa gaban mahaliccinsu a farkon kowane lokacin Sallah. Kowanne ɗayansu yakan ji girman Allah ga kowace gaɓa na kira zuwa ga Sallah har ya kasance zuciyarsa tana da cikakkiyar saduwa ga Allah Maɗaukaki. Ya zo acikin hadisi cewa:

*"Salloli biyar Allah ya hukunta su dole a kan bayinsa. Don haka duk wanda ya zo da su ba tare da ya tozartar da wani abu daga cikin su ba don rashin ganin muhimmancinsu yana da alƙawari a wurin Allah da ya shigar da shi aljannah"*

Aliyu ɗan Hussaini ya kasance idan zai yi alwala sai ya fita cikin hayyacinsa, sai aka ce da shi meye ke zo maka ya yin alwala? Sai ya ce: *''Kun san gaban wanda na ke shirin tsayuwa a gunsa?*

Hassanul Basari Allah ya ƙara masa yarda ya ga wani mutum yana Sallah yana wasa da gemunsa kuma sai ya ji shi yana cewa a cikin sujjadarsa ya Ubangiji ka aura min 'Yan matan cikin aljanna da za su zama jin daɗin ganina. Daganan Hassan ya ce kai wane! Ban taɓa ganin mai son 'Yan matan cikin aljanna da ke da ƙarancin kunya irin ka ba. Kana son 'Yan matan cikin aljanna a wurin Allah kuma kana wasa.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA:

1- Himmatuwa da cikakken shiri da natsuwa da hanzari domin yin Sallah.

2- Kiyayewa da yin sallolin farillai dalili ne na shiga aljanna.

3- Neman aljanna na buƙatuwa da sanin ƙa'idoji da girman ibada.

BABI NA BAKWAI

HALAYYAR MAGABATA WAJEN NESANTAR SHIGA KASUWA KAFIN KOYON ILIMI KASUWANCI.

Daga cikin halayyarsu nisantar zama a kasuwanni domin siya ko siyarwa sai bayan sun san hukuncin shari'a a dukkanin hulɗarsu da kuma tabbaci ga kansu da cewa ba bu wanda zai shagalta da kasuwa daga barin ayyukan lahirarsa. Domin duk abin da ya shagaltar daga barin Allah Maigirma ya zama shu'umi ga mutumin a cikin duniya da lahira.

Imam Malik Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana umartar masu mulki da su tara 'yan kasuwa da makiyaya a wurinsa. Idan ya ga wani daga cikin su baya da fahimtar dokokin hulɗar kuma bai san halal daga haram ba sai a dakatar da shi daga kasuwanci. Sai ya ce masa: '*'Ba kasan hukunce-hukuncen siye da siyarwa ba sannan ka ke zaune a kasuwa domin duk wanda ba shi da ilmi zai ci riba ko ya so ko bai so ba."*

Katada Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana cewa: ''Abin mamaki ga ɗan kasuwa ta ya ya zai kuɓuta alhali yininsa yana rantse-rantse darensa kuma yana ta lissafi.

WANNAN BABI YANA KOYAR DA ABUBUWA KAMAR HAKA

1- Kasuwanci da aikin gwannati da siyasa da kiwo wajibi ne sanin hukuncin shari'a kafin shiga cikinsu.

2- Jahilcin addini ga ɗan kasuwa ko ma'aikaci halaka ne ga kansa da kuma Jama'a.

3- Rashin shagaltuwa da kasuwanci tare da sanin ilimin addini a kai shi ne tafarkin samun aljanna.